[1:27PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: FUSKA BIYU Part 1
NA
HALIMA ABDULLAHI K/MASHI
Fuska Biyu 1-----1
NA leko a hankali ina sanda bana son mama ta ganni nasan sae tace na saka hijabi, in har kin ganni da hijabi, to ki tabbata islamiya ko sallah, don ko an matsa min nasa dana fita waje zan aiko dashi. Anyi fadan , anyi dukan , an gaji an barni sai addua inji mama. Na kusa kofar fita inajin mama tana fadin "ke! Ke!! Ke!!! Asma'u ai tuni na falla da gudu. Gidansu aminiyata Rahma zan je, ina sonta gashi ta juri zama da halina na masifa da tsokana, duk da ana cewa sai hali yazo daya ake abota, amma ni da Rahma ba haka bane, ita tana da gudun zuciya sam batason fada haka nan ita ma'abociyar sanya hijabi ce, duk kawar danayi sai mun bata, amma banda Rahma. Na kalli gidan dake kallon namu, maza ne zaune a barandar gidan kusan su hudu. Yaya Ali ne da abokansa a raina nace sarakan sa ido , riga da wando ne a jikina na jeans da farar shirt ko ince top, ta dame ni sai dan karamin gyale irin shigar da nakeso kenan a duniyata, kuma a ganina ban wuce wannan shigar ba, tunda yarinya ce ni 'yar sha biyar.
zan sha kwana layin su kenan sai gata, nace gidan ku fa zanje Rahma. kefa sai ina ? tayi dariya , nima gidanku zanje . nace to mu koma naku gidan wai ta ce a'a ni fa da shirin islamiya na fito , lokaci nayi sai mu wuce. naja tsaki to zo muje , amma Allah ban so komawa gida yanxun ba , tace saboda me? nace kin san Allah Rahma ban san me na ma yan gidanmu ba , duk sun tsane ni. tace ba tsana ba ce Asma'u , don nasan bai wuce ana miki fadan natsuwa ba. Na harare ta bansan me nayi na rshin natsuwa ba, kina nufin ban da natsuwa ko me? Ganin yanda na hayyako mata yasa tace , "Allah ya baki hakuri Asma'u , ba ina nufin ba ki da nutsuwa bane , kin san....."na katse ta "nidai yi min shiru malama zo muje in zaki. "muka taho sungun-sungun babu mai magana da wani, don ta mantar min da

fushina sai tace ina Suraj? nan ko na soma murmushi , nace daxun shine ya dauko ni daga makaranta. hirar suraj muke har gidanmu , ta nufi gurin su mama ni kuma na nufi dakinmu, don na daura zani akan wandona, nasani na nufi mama a haka laifin zai zama biyu
sai dai kash! ina isa dakin na samu su yaya yina masu cin ubana Anty Ainau da Anty fati da Anty salima, zan juya Anty salima tace "ke zo nan 'yar iko zo gidan uban wa kikaje a haka? nace "ni ba fa inda naje" na nufi sasansu mama ina yan kunkunai ku kun cika takura gara naje gun mama a haka bata da saurin hannu ku kam yanxun kun duki mutum. na samu Rahma su nata gaisawa da mama ta amshi rezar da mama ke yanke farce tana yanke mata. na shiga na dan rabe mama tace dago ta dube ni tace "yanxun Asma'u ba za ki taba jin magana ba? kin fi son kina yawo haka sai kace arniya? haka kika ga yan uwanki koko haka ki kaga Rahma tana yi? ko Aisha da take kanwar ki ta fiki hankali. na bata rai sannan na ce "to ni me nayi mama? ni ba a sona a gidan nan kowa sai yayi ta min fada" mama tace to sai ki rama mara kunyar banza , ba'a son naki me ake da mara ji? ki canja halinki mana ki gani in ba'a daina miki fada ba, karamarki dake sai shegiyar kafiyar tsiya , tace uban me aka miki zaki tsira min kuka? bansan shigowar yaya usman ba sai dai
sai dai rankwashi naji kus a kaina, yace shegiyar yarinya daxun uban wa na ganki da shi a mota ya dauko ki daga makaranta? ya kama kunne na baza ki rabu da dan iskan suraj din nan bako sai kin sha wahala? cikin kuka nace bafa ni bace ya usman, ya kara kai min mari ina wasa dake ne? ban sanki bane kenan? yasa kafa ya shure ni na saka ihun da duk yan gidan suka taru amma abin takaici babu wanda yace yaya usman yayi hakuri, saidai suce ya kara min gara ma su umma da hajiya sunce kece ai rashin jinki yayi yawa Asma'u, ace ayi ta fama da mutum? yi hakuri Usman, yace haba hajiya yarinyan nan ta fita zakka a gidan nan in dai kaji an kawo kara nan

gidan to ita ce. dazun fa motor yaron nan suraj na ganta ya dauko ta daga makaranta bayan Alhaji ya hana ta kula shi. mama ta fito tana fadin sai ma an hana ta, ta dubi yayunta mana su aina'u wa taga tana kula samari cikinsu? ina ce tun suna secondary duk wanda yazo gurinsu cewa suke yi je gurin mahaifinsu. amma ita da yake ta sa maza a ranta 'yar kankannuwarta yau ta tsaya da wannan gobe da wannan kai ranar dai naci duka tamkar.
ranar dae haka naci duka kamar jaka sannan na nufi dakinmu na kwanta a gadon mu ina kuka. rahmace ta ke ta bani baki har aka kira sallah nata tashi fuskata ta kumbura don kuka , nayi alwala nayi sallah haka ma Rahma, ta nufi dakin mama don shirin islamiya don can ta 'aje kayanta, nima na saka nawa duk gidanmu nice na dinka wando a kayan islamiya(not clear but ana fadin yanuwanta duk dogowar riga suke sawa na islamiya ita ta dinka wando ranar dae duk wanda xae mata fada xaece ta ringa koyo da halin kawarta Rahma har ta ji haushin ta ) ta biyo ta tana kira na ban tsaya ba sae tayo gudu ta same ni , muna fita lungun layinmu ta baya muka bi sannan muka kama hanyar islamiya, kamar daga sama nafa motar suraj na tsaya itama rahma ta tsaya yayi parking ya fito kyakkyyawan yaro dan masu kudi mai takamotoci na kece raini, ya nufo mu baby lafiya? na soma hawaye ya kama hannuna. oh please stop crying my baby
Rahma ta dube ni cikin takaicin yanda na tsaya ya rikr min hannu zomuje ka da muyi latti fa asma'u . nace ki tafi sai nazo. tace yanxun nan fa ya usman ya ce ki daina kula samar, na daka mata tsawa ina ruwanki? ta wuce yaja hannuna muka shifa mota ya share min hawaye da yatsanshi, fadamin me aka miki? nace wai ya usman ne yace na daina kula ka hrda dukana, yace to baby ke yanxun yaya kika gani zaki iya rabuwa dani ko ko yaya? ni dai gaskiya baby ba xan iya rabuwa dake ba, nace ai nima suraj ba zan barka ba bayan duk garin nanm kai ne kadai me sona, su fa ba wani sona suke yiba, yace to

mujr in kaki makarantar, yace bari mu dauki rahma, nace barta kawai itama yau haushinta nakeji. ina shiga ajinmu duk sauran yan ajin suka gyara xamansu dan bani guri. nice na zabi gurin kuma nace nan ne gurina duk da kasancewa kowa yana zam a ko ina, amma ana shakkar zama wurina , saboda masifata duk da karfi ne dani ba suna tsorona kasancewarbamu taba danbe ba shiyasa suke min kallon karfi.
na zauna ina tunanin yanda ba'a sona har zuwa san da rahma tazo. malam ya shigo yana rubutu. ba yabon kai ba, saidai ai min shaidar rashin ji, amma in dai karatu ne daga boko har islamiya nayi zakara. yanda malamai suka sanni da rigima haka suka sanni da kokarin karatu, wannan shi ne yas nake da farin jini cikin dalibai , suke kuma shakkata. hour kofar gidanmu motar ta tsaya, na fito tare da godiya tacemin zai zo anjima nace to sai dai yatsaya daga farkon layin a wurin wani gidan dake duban gidanmu ya Ali ne shi da wani wanda ban tantance shi ba , sai dai ina ganin kila shima dan gidan ne, yana ta min kallo mai kama da harara na wuce ina ce ma wanda ya rago min hanya sa anjima . yaya umar ya dubi kaninshi Aliyu yace, Ali wannan yarinyar yau ganina da ita na uku kenan, tana shiga gidan baba Alhaji itama 'yars ce? aliyu yace Asma'u? 'yarsa ce mana itace mara jin gidan, yace na kula daga zuwana shekaran jiya zuwa yau na lura bata da kamun kai, su Abubakar suka barta ta baci haka? Aliyu yace ai ya uwar yarinyar nan 'yar daru ce da taurin kan tsya.
[1:28PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1-----2
suna iya bakin kokarinsu. ya umar yace 'yar wacece a cikin matan gidan? Aliyu yace, 'yar mama ce ka ko san albasa batayi halin ruwa ba. ya umar yace 'yar mama? Ali yace kana mamaki ko? wallahi 'yarta ce daga ita sai aisha auta, ya umar yace lallai kam albasa bata yo halin ruwa ba, mama da dukkan yayanta salihai ne kai kaf gidan ma babu mai wata matsala shiyasa naje mamaki kaya matsattsu jibi atamfar dake jikinta yanxun tamkar tayi nishi su yage haka suke a

jikinta. Aliyu yace kaga kadan ma ba dan tana shan wahala ba ma kila da tsirara xata dinga yawo kuma ga smari kamar hauka yau wancangobe wancan, 'yar karamar yarinya jamilar gidan nan fa ta girme ta . ya uwar yace kai haba? Ali yace wallahi bata wuce 14 ba, ya umar ya mike ya nufi cikin gida yana fadin shi fa ganinshi an barta ne
ina zaune bakin gado inayin note shema'u ta shigo "Asma'u ki zo in ji alhaji " na dube tacikin faduwar gaba don nasan kiran babanmu dani babu alkhairi , kila ma an kai mishi karata , na ce to me nayi? tace oho in ce kina zuwa ko ko in ce baza ki zo ba? na harare ta sannan na mike. shi kadai acikin madaidaicin falon nashi yana zaune yana lissafin wasu kudade gefe yaya Abubakar ne da yaya usman, suma suna ta rubutu nasan harkar kasuwancin su ne. na zauna gefe nace gani Alhaji, a tare ya abubakar da ya usman suka jeho min harara sannan suka cigaba da aikn su. Alhajiya ajiye kudin hannunshi gefe yace Asma'u wato kina da kunnan kashi ko? a raina nace tome kuma nayi? yace tambayar ki nake yi?nace a'a yace me yasa ba kya jin duk abin dana gaya miki da wanda 'yan uwanki suke gaya miki? na sun kuyar da kai ya cigaba "na raba ki da yaron nan suraj amma kin ki ji ko? ke ba mashi ba ko wani saurayi na hana kin ki yarda duk yaushe kika tafasa har da zaki kone? wato baza ki dubi yayyanki ba babu wacce take tsayuwa da wani saurayi fa sai da izini na. ma'ana sai an gana dashi sannan na yarje musu kin ga suna tara maza saike?
to kiran da na miki yanxun na yanke hukuncin tunda ke ba zaki yi abin da nakeso ba to kema bazan miki wanda kikeso ba . tunda nine na haife ki ba kece ki ka haife ni ba, kuma ni da mahaifiyar ki baza ki sa mana hawan jini ba, don haka na daina biya miki kudin makaranta , na daina miki sutura , ke na daina miki komai ki dai ci abinci sadaka sannan shi wanda na rabaki da shi ki ka ki,sai ki ce masa ya fito, sadaki kawai zai bada a daura muku aure, ki debi yan kayanki ki bishi

allura bazan sai miki ba. tashi ki bani guri na
soma kuka domin duk iya shegena ina tsananin
son makaranta kuma ina karatu sannan nasan ina
son suraj amma munyi da shi aure sai na shiga
jami'a lokacin shi kuma ya soma aiki tunda
yanxun yana A.B. U zaria. (garin su xee lolz)
nace don Allah Alhaji ka tamake ni mana? ina son
karatu na , yace sanin kina son ya sani kuma zan
katse miki shi ba? yaya zan so abin dakike so?
alhalin ke da na haifa kina kin wanda ni nake
so ? zan kuma magana yaya Abubakar ya daka
min tsawa tashi shegiya.
dakin mama na zame ina cewa cikin ihu , ki
taimaka min
mamana don Allah zan mutu tace menene? na ce
alhaji ya cire ni
daga makaranta wai zai min aure bayan gasu
anty Aina'u nan su da
suke poly ai sune ma zasu musu aure ba ni ba,
na tsaya ina ta rusa
kuka, ta ce hakan ne ya dace da ke tunda ba kya
jin magana Asma'u
duk kin bi kin maida kanki 'yar iska kin zubar
mana da mutunci a
gari? da gudu na nufi dakin umma suna zaune da
anty fatima na
fada kan umma na ce umma ki min rai mana
Alhaji yace ya cire ni
daga makaranta ku roke shi na tuba ba zan kuma
yin komai ba, tace
so naea zaki ce kin tuba amma ai tuban muzuru?
tunda kin ja yayi
fushi dake ba shi kenan ba. jin ba sa'a na nufi
hajiya gara ita tadan
lallashe ni tare da bani baki kuma tace mu bari
ya huce sannan naje
na roke shi tare da daukar alkawarin daina
halayena, kai ranar naga
tsawon dareban fasa ba haka nan ban karya ba
bare na nemi kudin
mota, hasalima a sace na fito tun daga sabon
kawo har F.G.C malali
a kafa san da na isa har an tashi break sai dana

yi hawaye don
takaicin missing din darasi har. 3 yanda muke
shirin fara. test
dinnan.
haka da muka tashi bayan da Rahma ba tayi ba
akan na zo muyi
goyo a mashine amma naki, haka nan ta hakura
ta tafi su shema'u
da hadiza da Aisha suka hau mashin a gabana
hakan ya kara sani
yanke hukunci bani da mai kaunata duk gidanmu.
na iso badarawa
na gaji sosa na samu guri na zauna hutawa nake
yi can kamar daga
sama sai ga suraj cikin mota , ya fito yazo har
gabana ina kallon shi
ban ko matsa ba , yace nasha yawon nemanki
baby tun daxun naga
Rahma ta sanar dani kina tahowa a kafa kuma a
kafa kika je
makaranta . nace meyasa tace baki fada mata
ba, na dube shi duk
kan ka ne suraj, baba yace saidai ka fito muyi
aure na gama
makaranta ba zai kara biya mun ba, yayi shiru
bayan ya tsugunna
kusa dani, yace to yanxun yaya zamuyi? nace
shine ban sani ba, yace
yanzun dai taso muje na ce, a'a yaya zan shiga
motar ka? a kuma
ganina? yace sai na sauke ki bayan layinku , na
mike na shiga a
hankali muke tafiya, tare da neman mafita a
karshe muka yanke
shawarar zamu na haduwa a bayan layinmu kuma
ba zai dinga zuwa
da mota ba kuma yace ko ma nake so na
tambaye shi zai
na tambaye shi zai min yace ma zai saya min
waya sai na boye ta mu dinga magana, son da na
shiga gida ana sallar la'asar ban kula kowa b ni a
dole ba'a sona na daina kula kowa haka na yanke
shawara nayo alwala nayi sallah nasa kayan

islamiya Aisha ta shigo. Asma'u kizo inji mama, na nufi dakin na shiga a raina nace nasan dai laifi nayi tunda dama nice uwar 'yan laifi mama ta dube ni ga abinci nan a kicin tun da yake ke kn fi karfin ki manamagana 'yar gaisuwar da kike mana a raine yau bamu samu ba, idona ya ciko da hawaye na ce na koshi , tace to ai shi kenan kila mai hure miki kunnan ya baki wanda yafi namu an hana ki zuwa makaranta amma don ki nuna ma duniya cewa bamu isa. ba kin tafi, na soma sharar da hawaye cikin shessheka na ce mama na ga ne term bai kare ba kar ayi asarar kudin mama tace ina ruwanki , me biyan yace ki daina zuwa ko sai yaje har makarantar yasa an goge sunanki zaki daina zuwa? ba tare da na sake wata magana ba, na mike na nufi dakinmu , na cire hijabin na kwanta kan gado ina mai tausayin kaina tare da tunanin anya kuwa gidannan ba tsinto ni suka yi ba?
banyi tsammanin haihuwata akayi yi ba,kila ni ba 'yar asalin cikin gidan nan ba ce. nayi kuka har na gaji ga yunwa amma nasan ko na tasa abincin ba zan iya ci ba, naji an zauna kusa dani an dafa ni ko da ban juyo ba nasan cewa Rahma ce . na dago na dube ta tace "Asma'u me ya hana ki xuwa islamiya? nace cikin kuka an cireni da sauri tace an cire ki? nce har boko ma, saboda me? nayi shiru ta kana ni tashi ki gayamin nasan zaki dan ji sauki in kin gaya min kila ma mu samu mafita jin haka na tashi zaune na koro mata komai tayi shiru na dan lokaci sannan tace Asma'u xan gaya miki gaskiya, duk laifn ki ne menene wuya cikin yi kaza bar kaza? duk shine ya janyo wadannan matsalolin nace ni yanxun yaaya xanyi tace ki bar makaranta a kaman kwana 3 sannan kije ki ba alhaji hakuri ki gaya mishi kin daina kuma ki rabu da suraj.sai dai bazan boye miki komai ba rahma, ba zan iya rabuwa da suraj ba, tayi shiru cn tce to sai ki cemasa ya dan daina zuwa tukunna nace saidai hkan, can tace Asma'u zan tambaye ki, donAllah wani abu. bay kuw shiga tsakaninki da suraj dinnan?

[1:29PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1------3
na dube ta kamar yaya? ta dan yi shiru sannan tace, kiyi hakuri yanda naga yake rike ki sai ina ganin wata rana zai iya neman ya sanki matsayin ki na 'ya mace , na ce Rahma mutane da yawa suna min wannan kallon amma ba haka ba ne, yan layin nan ma 'yar iska wasu suke ce min, niko ba haka nake ba har yan gidan nan kallon da suke min kenan . a layin nan. ma na lokacin da nayi ciwon nan? tace eh nace akwamasu cewa an cire min ciki ne. rahma tace saboda irin shigar da kike yi ne Asma'u , ki daina an fa taba takawa ba so daya ba ba biyu ba, aka ce momynah ta rabani da ke , ke 'yariska yarinya ce, momy tace Allah ya shirya ita ba ruwanta, nace duk masu min sharri su da Allah . rahma ta ce kema ki kiyayye abin da za'a zarge ki , nace ni raba ni da gulmar mutane yanxun me zai wanke ni daga zargi sai Allah .
yau kwana na takwas rabona da makaranta na fito zanje kitso jikina riga da skirt material ya dme ni tmkar zasu yage,in nyi kwakkwaran nishi duk kayan haka suke don an mana dinki zan dauki nawa in je a rage su, ya uwr ne yana kokarin hawa mashin jikinshi d kaki sojoji, wata randneniyr mashin ce ban taba ganin irin ta ba ya galla min harara nan take nima na rama a raina nace don kana soja zanji tsoranka? na tsallaka dayan gefen da gudu ya kwaso mashin din ya bi ta ciki wani ruwan tabo duk ya fancale ni da ruwan da karfi nace Allah ya isa ashe yaji , nan ya dawo ya dauke min fuska da mari tare da fadin 'yariska mara kunya.
na dauki alwashin sai na rama , ai wannan cin zali ne. ga bata jiki ga duka? daga nan ban kuma ganin shi ba har sati biyu , sai wata rana suraj ya dauke ni mun tafi shan ice cream a gamji , dama unguwan dosa muka hadu ya daukeni saboda yanxun baya zuwa layinmu yana ma makarantar shi , sai weekend yake zuwa , snye nake da riga da wando na jeans yana rike da hannuna muna tafiya muna hira ina zaton ramar sojoji sunyi wni taro anan wani hall dake nan gamjin , sai hangen ya umar naayi ya tsaya yana kallonmu, daidai

lokacin suraj ya tallabo nii zuwa gefen kirjin shi ya girgiza kai ya wuce nace suraj zo mu tafi wancan mutumin yaron abokin Alhaji ne kuma layinmu daya ka da yaje ya fada nan muka dawo a raina na tsani ya umar, ban ma dade ni da sanin shi ba wai ashe tun yana karaminshi yake karatun soja tun bayan da yagama primary, yayi karatun soja sosai yanxun yana aiki ne a port harcourt , wani course yazo kd yana jaji shi ne ya kanzo gida.
Alhaji Ahmad shine mahaifinmu mijin mata 3 mama itace uwar gida kuma auren zumunci. su 'yan asalin gombe ne , fulani ynxun haka dangin su suna can kasuwancin ne ya kawo shi nan in da yake saida zannuwa , atamfofi , laces, shaddodi, da sauransu . a yanxun shagunan sa 3 cikin central market . mama tana da yara 8, yaya abubakar, ya usman , ya mas'ud, yaya sani, anty aina'u , anty fatima, sai ni is auta Aisha, ita ko umma 'yar kano ce kuma a can ya auro ta duk dai gurin harkokin kasuwanci suka hadu 'ya'yanta 3 shema'u sai hadiza sai hamza, shema'u sa'a ta ce ta dan girme ni amma kadan, hadiza ce babba. ita ko hajiya A'I makka suka hdu , ance auranta 4 bata haihuwa ba sai data auri Alhajinmu , tashin farko ta haifi yan biyu hassan da usaina , yanzun tana goyon gambon su .
yanzun tana goyon gambon su , Ahmad sunan Alhajinmu muna ce masa khalifa. mama mace ce mai tsananin son zamn lafiya , na yarda mace ta gari ita ce sila ta zaman lfy , domin duk yanda mutum yaso ta shin hankali ba zai yi da mama ba, tana da tsananin gudun bacin zuciya , tare da ibada ga biyayya ga miji ga kuma tarbiya mai ban sha'awa da take ba 'ya'yanta wannan yasa kishiyoyinta suke girmamata tare da sakar mata duk wata shawara ko 'ya'yansu suna matukar son mama. Ya abubakar da ya usman babu nisa tsakanin su , don haka tare suka shiga makaranta tun daga primary har zuwa jami'a , sunkaranta degree dukkansu fanni kasuwanci da suka gama basu nemi aiki ba sai suka fada kasuwanci gurin

Alhaji inda ya bude musu wani tafkeken store kayan kwalama dana shafe shafe zuwa suturu akan titin isa kata dke unguwar sarki , yaya mas'ud da yaya sani yanxun suna b u k , Anty aina'u da anty fatima suna poly, hadiza tana ss1 fgc malali, shema'u js3 Aisha primary 5
hamza da yan biyu suna pri 1.ba yanda xaka gane wannan dan wannan ne babu bambamci koh 'yan ubanci, ni kadai ce matslar gidanmu, kamar yanda suke cewa na fita zakka, ni dai tunda na taso nafi son wando fiye da zani ana sai min wanduna amma dana soma tasowa mama ta hana sai dai siket in ko aka dink min zani sai naki daurawa insa riga in ta yawon daga ni sai pant sa rig, wannan yasa ake dinka min siket da na kara wyao in an dinka min sai na kai nace yayi yawa wai a rage, gani tubakallah yarinya ce ni amma ina da diri mai kyau kuma kafatanin gidan mu farare ne yaran gidan nice baka, sai dai naji ana cewa duk nafisu kyau. tun ina js1 maza suke sona wannan yasa na soma tunanin ko dn nfi 'yan gidanmu iya ado ne, d nuna jki su anty aina'u basa tsayawa da samari har suka gama secondary skul, sai yanxu kuma gurin alhaji suke turo duk wanda yace yana son su kamar yanda mama take ce mana duk wanda yace yana sonmu to mu turo shi gurin Alhaji su take gaya ma don tace ba'a zo kanmu ba
yanxun haka duk suna da wadanda zasu aura Anty aina munnir dan sokoto ne yana aiki ne a nnpc kd, is anty fatima , Aminu yana nafdac lagos , hadiza dai ina ganin Aliyun gidn Abba zata aura naga yana dan kiranta. Abba Aminin alhaji ne dan sun wuce abokai. abba dan bauchi ne mutumin azare , kuma tun a gombe suke abotarsu , har yau. Abba shine silar zuwan alhaji kd. Abbba yayi karatun boko mai zurfi kuma ma'aikaci ne bai dade da yin ritaya ba, saboda abota ne suka yi gidanjansu layi daya sabanin d abba 'yan unguwar sarki . Alhaji yana unguwar dosa sunan Abba Alhaji muktar , yana da mata 2 uwargida momy kawar mama ce kut da kut , babban yaronta soja ne umar yana port ya girmi yaya

abubakaar din gidin mu sai aliyu dan bata
haihuwa da wuri tsakanin umar da aliyu shekara
9 , Aliyu ma'aikaci ne. bnkin phb sai anti salima
zak zata yar mamace saboda kusn ma a gidanmu
take, sai nafisa sa'ata sai yan biyunta hassan da
usaini, na manta da jamila daga itace sai nafisan
jamila ce sa'ata koma nace kawata mama ce
tace ta daina bina kar na bata ta , mamanmu
[1:30PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1------4
Ya umar tunda mugu ne yanda naji su anty
salima dasu anty aina suna lbr tun suna kanana,
ysha basu wahala musamman inkn ci na 5 a
makaranta zuwa sama, amma daga na 1 zuwa na
hudu yana maka uzri inko kaci sama da haka
ayya sunan ka sorry, zai zane ka tas ya saka ka
kallon rana irin da mugancin su na sojoji. wata
rana su anty fatma da anty aina sunjehutu gidan
shi ma yazo hutun, ayya sun sha wuya , yana
zaune a falo yana kallon kwallo. suma suka
zauna yace bakun zaunaba saura naji surutu,
dama ina ciki daku suka yi tsit suna ta kallon
kwallo anty fatima tace ni dai nafi son masu
fararen kaya su ko anty salima da anty aina'u
suka ce sunfi son jajayen, ashe shima yafison
fararen wato asnal.can jajayen suka ci, hu suka
soma fatima sun ma manta da batun yaya umar
yana ciki, haushi 2 ya kama shi ga haushin anci
garin shi ga ihun su, nan ya had kan anty salima
da anty aina'u ya gwara sannan yasa ka su
zaman mashin da tsallan kwado sun yini suka
kuka dan sun gaji a karshe ya musu bulala 20.
ni kuma in sun bani lbrn shi sai ince ce ya rana
ku ne ina ma lokcin ne da sai na nuna mishi
nawa taurin kan, anty aina'u tace ai da yanxun ne
shi ne maganin shegen taurin kanki in ce sai dai
mu zuna shine yanzun ya soma nunamin? y jika
ni sannan ya mre ni? zan rama. yau kusan
watana dy da daina zuwa makarant kullum cikin
roko nake har anyi jarabawa bana nan , ranar ko
anyi kukan d dukmai sona sai ya tausaya min
amma 'yan gidanmu ko a jikinsu. Alhji ma da
mishi maganar yayi hakuri na daina sai yace ai
ban rabu da suraj ba, saboda haka sai dai in suraj

din ya fito ayi auran can naci gaba da karatun gidansu. na shirya zanje gidansu rahma kuma inason ganin suraj dan in san yanda zamuyi, tun daga abin da alhaji yace , cikin sa'a ina ftowa sai naga mugunnan ya umar, suna magana shi da wani abokinshi ne ko yaya suke oho, duk suna sanye da kaki, na koma cikin gda hadiza tana wanke wanke kwanuka, na suro an sannan nazo na antayamishi tsayawa sukayi suna kallona, nace kima kaji inda dadi, ya Aliyu kaninshi dake can bakn gate din su ya taho da sauri yana fadin ke karamar mara kunya shi tsaronki ne?
nace ehdin kai kuma ina ruwanka?zai kai min mari ya umar ya rike shi yace barni da ita kada kayi fada da karuwa....mutuncin ka zai zuba na san maganin ta , kinga yanda kika jika kakin nan sai kin wanke su, so dari nace ba so dubu ba? ai sai ka sani na wanke, ya ce ayya ai baza ki iya ganewa bane , sai randa ki ka fara mara kunya , karamar karuwa , kalmar da tamin zafi kenan na kara tsanan shi, wai ni ce karuwa nace eh to karuwar ce naga dai ba jikin wani bane koh? na koma gid cikin takaici , abokinshi yace amma aminina yarinyar nan bata da kuny , yace barta zata gane kurarta,kasan mata ba abin fadan soja bane, zan azabtar da ita ta manta hanya. a daren ranar muna tare da suraj ya bani waya kirar kamfanin samsung yar mai kyau da layinta duk gidanmu su ya abubakar ne ke da waya sai alhaji sai ko landline da ke falon kowacce matar gidan boyeta nakeyi cikin wando suraj sai ya kirani musha hira inba kowa a dakin. gaskiya inason karatu na , don haka na matsa ma suraj inaso mu gana, muna cikin motar shi ya dube ni menene kike son ganina baby duk ya kosa
menene kike son ganina baby duk na kosa dare yayi danna amsa kirar gimbiya? mata na dan hada rai yace bakiyi kyau ba,ya juyo da fuskata gayamini mana sweetynah, nace nifa na gaji da sauri yace dame? nace da zama babu karatu ba zan boye maka ba tunda alhaji yace ka fito, to ka turo kawai ayi auran in yaso sai naci gaba a gidanka , tunda yanxun yaki, 'yan gulma suna

gaya mishi muna tare. yayi shiru na lokaci can
yace kin san yanda muka yi ta kai ruwa rana
dasu daddyna kuwa? ban gaya miki bane saboda
banason hankalin ki ya tashi sun dage kan cewa
ban isa aure ba wai 21yrs me zance ma matar?
kinji fa yanda nake jina garau ko 4 suka zuba
mini. ai zasu sha mamaki , nace ni dai yanxun ba
wannan ba mafita nake nema, tunda nima ai da
saurana , auran dan dai rashin gata ne yasa za'a
min yace. to ko in canza miki makaranta? na a'a
wai raba ni ai kilama sai su mama sun tsine min
duk mukayi shiru , a ranar dai har kusa 10:30
babu mafita kafin daga karshe mukayi sallama
akan kowanne zaiyi tunani
Abba ya daga kofin shayi yana sha kuma gefenshi
anty ce amaryar shi yace kiramin hajiya ta mike
ta nufi dakin hajiya anty haka yaran gidan suke
kiranta bata taba haihuwa ba tana matukar son
'yakyan mijinta dayake ance mai da wawa na ne
yasa suke matukar zaman lfy da momy hakan
nan ya umar dan dakinta ne yanxun nan zakaji
suna hada plan akan wani abun in ba'a son Abba
yayi fada bayan sun dawo sun zauna , abba yace
hajiya Aisha kin san dalilin kiranki? tace a'a yace
na gaji da zaman umar haka, na bashi dama ta
farko na bashi na biyu , na kuma nashi na uku
wannn karon na gaji xan nemar mishi mata.
momy tace gara haka ni kaina nayi nayi yaki
saurarena amma ga anty tashi nan ina ga ita ce
zata fini sanin meke faruwa? tunda itace abokiyar
shawarshi yayi murmushi ya dubi anty tasu yace
to ke anty su yaya kuke ciki da dan gidan naki?
ya zama tuzuru anyi karatun anyi course din har
so nawa am kuma aiki sai me? momy tace sai
aure, anty tace kada ku damu, yarinyar da muke
so ce tana kartu da a son ranmy sai in ta gama
ya zama daidai da mun kammala gininmu
Abba yace a'a wannan katafaran gidan na umar
ya mishi kadan? anty tace ba nufin mu kenan ba,
abba yace to ku sake shawara na baku wata 2 in
lokacin ya cika babu wani bayani zakuji nawa
bayanin maganar yarinya tana karatu ba ayi da
aure ne? momy tace yi kai yace to. donhaka

wannn cekarshen magna, anty tayi dariya tace munji abb insha Allah zakaji mu kafin lokacin dakaba mu . Na samu da kyar da taimakon hajiya da umma Alhaji ya yarda na koma makaranta bayannasha tsauraran dokoki nace wa bani ba suraj ,bani ba kananan kaya sannan in daina tsiwa na yarda duka zan bari amma banga zan iya ba, na koma makaranta cike da murna da farinciki.surajkam muna tare sai dai a waya, waya cikin sirri na rage saka wanduna sai dai riga da siket suma din damammun ne sai dai yan dan fi wandon haka yasa wasu sakar min fuska ganin su na shiryu.
ya kishin gida bayan ya aje kofin gilashin da ya gama shan juice yanxu ya ciro wayarshi ya soma neman antynshi ringing na 2 ta daga yace Allah ya bar min antynah ya gidan? tace Ify ba lau ba , ya gyara zama me ke faruwa a gidan? tace abba ya bamu lokaci yace wata 2 in mun wuce haka za'a mana auren dole , ya saka dariya auren dole anty ai na wuce nan, ta sak. dariya da gaske Abba keyi har momy fa, yace ai momy ita ce ta zuga shi anty tace menene Ibrn farida saboda gara asan nayi fa? yace tun wancan satin muna tare babanta ne matsalar yace bai yarda tsarin ana aure ana karati ba, ni kuma gaskiya inason yarinyar sai kinganta antyna , tana da kyau ga ilimi ga hankali, ga kamun kai samun kamar farida sai an tona
Anty tace guri yayi nisa ne shiyasa ban ganta ba , yace hakane amma kinsan yanda zamuyi? tace a'a zan kirata a way,inji in har tana nan port din zanje mu ga yarda za'ayi Anty tace ya kamata ka sani ne? yace a'a tace kace manyanka zasu zo in yaso in sai a saka lokaci zuwa sanda zata gama makaranta yace kin kawo shawara antyna saidai nazo karshen wata suka ajiye waya tare da fatan alkhairi ga juna
ina cikin saba sabulu naji wayata dake gefe ta soma ringing nayi sauri daukar zanina na goge hannuna jikina kam duk kumfa na daga wayar ina tsoron kar wani ya jiyo ni , nace suraj yaya ne? yace zakije party dinne? nace wanne kuma? yace

na faisal kin manta ne? nace oh birthday din
faisal kake magana? yace eh, zanje mana yace
yauwa har naji dadi saboda kinsan in an tashi
daga na gidan su akwai wanda muka shirya mishi
iyaka mu friends da beb dinmu, a maharaja hotel
nace duk a yau? yace eh na gidansu xa'ayi 3
zuwa 6 mu kuma 8 zuwa yanda ya samu nace
zanje is dai kasan yanzu an samin takunkumin
yawo kuma an amshe min wanduna na yace dan
wannan karki damu zan sai miki wasu in mun
hadu sai ki saka nace to zan san yarda zanyi in
fito ko ban samu zuwa na gidan su ba sai muje
chasun , yace haka ne tawn me kike yi ne yanzu?
nace wanka fa nakeyi yayi driya kiyi da kyau
babynah , nace take care, da sauri na karasa
wankan na fito ina shafa mai ina tunanin irin
karyar da zan sheka dan na samu fita da dare,
gani da son party.
[1:31PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1-----5
Gani da son party rawa dama sai kace indiya ta
haifi ni, ranar dai na rasa mafit hour magrib, can
dabara ta fadomin na samu mama a daki nace
mama zanje in gaida momyn su rahma bata da
Ify , ta dube ni zani da riga na saka ga wani
zumbulelen hijabi na shema'u ne ma nasaka
fuskarta ta nunamin taji ddin hak , sannan tace ki
gaida ta nim zanje na dubata , nace to ina fitowa
suraj na min waya, na dauka yace kin samu
fitowa kuwa? nace eh ynxun na fito amma zanje
gidan su rahma kasan da ita nayi karya, yace to
in kin fito gidan su ki same ni a karshen titin
laynsu nace to, mun gaisa da momy sannan naje
gun rahma mun dan taba hour inda ta nunamin
jin dadint da ganin shigar da nayi cewarta wai na
fi kyau, nace zan tafi tace da sauri haka? nace
ina note ne fa kika fadomin a raina naji ina son
ganinki shi ne akace kar in dade, kin san an
samin takunkumi, tayi dariya sannan tace bagashi
ba ana ganin cin nasara? nace haka ne zan tafi
in kinzo gidanmu mama tace ya jikin momy , kice
da suki tace naje na ma momy sallama ta rakani
ni hanya
Ta rakani hanya nace ta barni nan tace to mukayi

sallama na sameshi yana jirana cikin nota na
shiga sai gidansu yau ce rana ta farko dana taba
zuwa gidan su suraj dake badarawa.
tangamemen gida mai matukar kyau, gefenshi
daban ne yace bari muje ta can kusa da dakina
kada a ganmu nace to na rude da kayan da suraj
ya sai min, kaya ne hadaddun babies duk kala
hudu ne amma babu riga dake da hannun arziki ,
wata ma iya cibiyata, ya soma cire min hijabi
yana fadin gwada mu ga wadda zatafi yi miki
kyau, kin san zanfi so ki fi bebs din gurin kyau,
nace nima zanso haka na kwashi kayan nace bari
na shiga nan in na saka sai nazo in nuna maka
ko? yace in kinfi son haka shikenan amma inkn
gwada a gabana cinye ki zanyi? nace a'a bana
son kallo ne. (kawata ta birgeni) duk sun min
kyau amma suraj yace na saka wanda tafi matse
ni , tun da shi rigarshi tana da hannu daya kuma
yafi son rigar nace suraj duba fa cibina a waje
haka duk kirjina a waje yake yace ai shi ne
hadewar nan na yarda nace gashi ba takalmi d
kayan makeup yace karki damu bari na sato miki
na mom dina kiyi makeup din
Takalmi da jaka in mun fita sai mubi ta wani
store din ki zaba, ya fita da sauri sai gashi dasu
munata dariya , nace amma ka iya sata naga
kana fita har ka sato, yace ai tana dakin dad
shiyasa, na taje gashina yayi kyau na kama na
dubi madubi nayi kyau matuka saidai nayi kama
da 'yan iska (Allah ya shirya) haka nace ma suraj
yayi ta mun dariya yace in anyi auranmu kayan
da zan dinga saka mishi kenan yana gani nace na
yarda kai tun a cikin akwatuna kada kasa atamfa
ko leshi zaka zuba, yayi dariya yace kinga munzo
da sabon salo kenan ko? nace za dai musha
surutu ne, yace ayi tayi muka fito ya canja mota
glass dinta mai duhu ce 'yar kucila toyota ce,
muka fita sky store muka shiga na zabi wasu
shegun takalmi masu tsawo da jaka bakake nan
na kara fitowa na zabi sarka da dan kunne
fashion na yan gayu sannan muka dauki hanya
San da mukaje guri yayi guri zuwan mu sai ihu
ga bigboy ya iso haka abokanshi suke kiranshi,

nan fa naga bebs 'ya'yan masu kudi sai dai nasan duk da sunfi mu kudi ba mai nuna min kudi da body, da iya ado.don haka nima sai naji kaina yayi sama ai nima wata ce kuma suraj din suna da kudi fiye da suran ashe ma shine shuganan hada partyn. don haka sai na shiga duban su da dai bayan kyar gabatarwa da dan abin da ba'a rasa ba sai aka shga casu, nan fa da yawa 'yanmata suka sallama min samban san dare yayi ba ashe sha biyu, kuma na soma tsorata da yanda naga wasu yarinya da saurayi anyi cikin wani daki, suna manne da juna. kuma a dakin dundum da duhu duk sai na tsargu don ni iskancina bai kai nan ba, don hka sai nace suraj zan tafi gida, yace ki dan bari mana dare gurin ya gauraye da duhu an kashe wuta. suraj ya rungume ni babyna nefa sun dauke wuta, nace muje ka kaini gida don Allah kasan fa da wayo na fito, kmin na karasa sai naji hannu a kirjina da saur nace menene haka suraj? na bige hannun sai nake jin nishin mutanan gurn wani gurnanina fahimci wato masha'a akeyi
Nan na soma laluban hanya, suraj yana rike dani nace sake ni tafiya xanyi nan ya soma min korafin banason shi, shi yasa banason yana tabani nace wace irin tabawa ce baka yi min suraj? sa rai fa nason Allah ya hana amma saboda son da nake maka da kuma yanda banason bacin ranka na barka kana tabani na fit waje kafin na fitan ma sai karo akeyi da mutane. suraj ya biyo ni yana ta faman bani bak ya sha gabana ya rike min hannuwa, lallashina yakeyi har da hawayenshi wai yana cikin wani hali in taimaka mashi nace gaskiya suraj ba zanyi zina ba, na kwace hannuna na tafi , ya tsaya yana kallona, can yace baby in nayi da wata baza ki damu ba? ko juyowa banyi ba bare in bashi amsa gabana ke mugun faduwa ganin hanya shiru, lallai dare yayi na ciro wayata ina duba lokaci 12:30 na dafa kirji nace na shiga 3 ! na kara sauri titi na mika babu kowa sai motocin dake wucewa jifa jifa.
Wata mota ta tsaya da sauri na isa gurin dan

neman taimako samari ne guda 2 a ciki suna shan sauti na bayanne yace shigo mana baby nace taimako nake so sabon kawo zanje , suka ce shigo mun kai badarawa sunata min surutan banza, hardai na bayan ya soma dagamin kafada tare da fadin baby ko zamuje mu dan huta na awa 2 kacl ni awa 1 abokina awa1 ? na dube su cikin takaici nace, ni ni ba 'yariska bace da zaka ce muje a huta , sai naga sun hada ido sun kwashe da dariya. direban ya ce haba yarinya duk wanda ya dube ki yaga cikakkiyar karuwa sai dai in zaki mana rowa takaci ya kamani nace kune dai yan iska bani ba, suka ja suka tsaya ke 'yar bariki kada ki gaya mana magana, sauka nace sai me in an saukan na fita suka ja motor nace 'yan iska kawai.
Tafiya nake har ma bansan gurin da nake jefa kafa ba, sai jin taka birki nayi quuu a bayana kan in kauce har motar ta bangaje ni sai gani a kasa, fitilar motar ta dallare ilahirin gurin da haske, ban tashi dga kasan ba naji taku tafiyar mai motor tsoro ne ya kamani a raina nace kilama dan yankan kai ne, takalmin shi na fara kallo gabana ya fadi na dubi wandon soja ne , na fada a raina shi kenan zai kasheni da duka, yce ke na dube shi da sauri saboda muryanshi dana ji gabana yayi mummunar fadywa na'am na ambata ya umar jikina ya soma bari yace ke me sunanki ma? nayi shiru ya dakamin tsawa ya sunan ki nace? nace asma'u , yace tashi da tsawa yakemin magana na tashi yana dubana tamkat yaga kashi cike da tsana yace lallai yarinyar nan kin fita daga sahun kananan karuwai kin koma cikin manyansu, lallai an jibga asarar haihuwa wannan ai gwara barinki da haihuwarki, amma bakiyi halin mama da alhaji ba kai kaf gidanku kece fitinanniya banma san sanda aka haifeki ba, amma har kin kware da bin maza yaja tsaki tare da tsirtar. da miyau ya wuce ya shiga motar shi
Hakika naji zafin zagin da ya umar ya min, amma hakan bai hana ni yin saurin zuwa kusa da kofar motarshi nace ka taimaka min ya umar don Allah gida zani ya mini wani kallo sannan yace god for

bid in dauki najasa cikin motta? bani ba ban kasance mazinaci ba ba zan dauki mazinaciya ba ya tada motarshi tare da fadin ba kwanan gida zaki je ba? dan rashin imani irin na soja haka ya uwar ya tafi ya barni . ina tafe ina kukan bakin cikin zuwana gurin partn nan nayi nisa da tafya naji wata motar na kauce kar a buge ni, ashe suraj ne haushinshi ya kama ni ya tsaya yana baby zo muje in kai ki gida nayi mishi banza naci gaba da tafiya, yayi parking ya fito haba baby yi hakuri nima sai daga na gane ban kyauta ba, na tsaya danaji haka ya iso zo muje nace kaje kayi da wata dinne? yace iye, a'a haba dai ya shiga 'yan kame-kame naje na shiga motor na ce dubi time suraj kai baka damu ba ko kashe ni za'ayi kashe yi ko? yace a haba yanzun dai ya zamu yi? nace ina kayana , yace gasu can gidanmu, can muka wuce na can za sannan ya kuma dauko ni har maigidansu
Har maigadinsu yana ce mishi surajo ina zaka da dare nan yace yana zuwa. tun kafin mu kai gidnmu muke ta neman mafita a karshe ya kaini wani kemin aka dan sa min bandeji a ciwon da naji na kafa sakamakon bigeni da ya umar yayi sai ya kaini gidan wata kawar mama dake rafin guza yace wai ya buge ni ne shi ne na suma to ban farfado ba da wuri sai yanxun shi ne yace ina ne gdanmu na ce rafin guza , na nuna mishi nan gidan nayi shiru na sunkuyar da kai ina mamakin yanda suraj yake tsaro karya . hajiya rabi ta kama dama ta mijinta ya rasu daga ita sai 'ya'yanta shi yasa nace ya kaini can, ka bugu biyu zuwa na uku ta bude gnina yasa ta shiga rafka salati tare da tambayar ko Ify? kafin nayi magana suraj yace ko kin san wannan yarinyar? tace kwarai 'yata ce nan ya shga koro mata karya ta hau kai ta zauna musamman da ya nuna mata plaster kafata . ta shiga gero mishi godiya sannan ta jani cikin gida, kafin na kwanta sai da hajiya rabi tadafa ruwan zfi a kettle ta gasa min kafar da nake ta dingishin karya , nayo wnkasannan
Nayo wanka sannan ta tambaye ni yanda abin ya

faru, nan na karkacr na sharaara mata karya da
cewa ina tafiya n dwo gidan kawata kawai sai
naji taka birki ko kafin in ankare har motar ta
bugeni, daga nan ban kuma sanin komaiba sai a
kemis ni fa ma bansan sanda nace mas a rafin
guza gidanmu yake ba, sai da naga mun shigo
unguwar sai kuma Allah yasa na nagane nan
gidan barka da arziki hajiya rabi ke ta yi min.
kafa 'yar albarka dana dinga liliyata cikin dare
don ta kumbura kan safe har ta tashi gurin ciwon
yayi fushi ya kumbura , don haka nayi murna
sosai sanda muka isa gidanmu tuni hankular 'yan
gidanmu ya gama tashi banda maama wacce ta
ce yawon iskancina na tafi, har umma da hajiya
suna cewa ta bar cewa haka yanxun duniya ta
lalace. bayan an gama karade unguwa da
nemana sai gamu mun iso ina ta dingishi . hajiya
rabi tana min sannu.'yan gidanmu suka biyo mu
dakin mama suna tambayar meya faru? na yarda
da haj. rabi in dai gurin bada kanu ne, domin
yand take rattafo zancan babu mahalukin da zi ce
ba' gabanta abin ya faru ba,
[1:33PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----6
Su anty aina'u da umma da hajiya sun tausya
min sabanin mama wacce tace ita wannan zncen
bai shige ta ba, na dai tafi yawon iskancina ne.
jin hakan yasa naa fashe da kuka tare da rantse
rantse cewa mota ce ta buge ni, umma tace haba
mama yarinyar tsautsayi ya same ta, mma kice
haka? hajiya rabi kuma mikewa tayi tana fadin ni
kinga tafiyata don na kula bamma miki gwaninta
ba . mama tace haj.rabi ba nufina kenan ba ,
nagode hajiya rabi tace dama tun jiyan take min
kukan tasan kila ace karya ne. hajiyan gidanmu
tace wani irin karya? nan dai mama tayi shiru ba
don ta yarda ba sai don ganin babu wanda ya
goya mata baya. haka makota suka yi ta zuwa
jaje amma da yawa gulma ce ta kawo su, Ibrn
ma sa canza shi akeyi har da masu cewa an sace
ni ne, dayawa dai sunce party naje yan sanda
suka kawo hari gurin gudu mota ta bige ni, nace
kowa dai yayi ya gama ni dai dama Alhajinmu
nafi ji kuma tunda ya yarda har da kaini asibiti a

duba ni ko na bugu a wurin gurin mama ko haushin maganar takeji domin ta hakikance karya ne.
Momy da anty suka gaisa da mama tare da mata jajen kade ni, tsaki mama taja sannan tace kema hajiya aisha kin yarda? wannan zancen karya ne momy tace haba ke ko maman su aina'u me yasa zaki dinga biye ma surutun 'yan unguwa? duk da rashin jin asma'u ai ba zata prtyn dare ba, dn 'yarki ta samu hatsri shi kenan ki bita da mugun zargi, anty tace Allah ya shirya mana, mama ko cewa tayi dama aike tuni baki son laifin asma'u hajiya Aisha momy tace ai ni 'yar gidana ce duk cikin yaranki babu wacce nakeso kamarta. mama ta ce lailla don ba zaune kuke guri guda da ita ba, sun fito mama ta dan tako musu suka tafi gida suna shirin shiga ne anty tace momy ga motar dan gidana yaushe ya shigo kd? mama ta dubeshi yana kokarin parking tace kila ma nan ya kwana ya karaso cike da fara'a yana fdin daga ina ku ke? momy ce ta soma cewa Allah sarki yarinyar nan ce 'yar gidan hajiya saude tsautsayi ya same ta, yace 'yar gidan mama? tace eh yace aina'u ko fatima? anty ta amshe da cewa asma'u din nan, itace wai mota ta kade ta ta suma har ta kwana gidan wata kawar mama din
Mamaki ya cik shi yace yaushe? momy tace shekaran jiya da dare, zuwa gidan kawarta gada maman kawar an ce bata ma dade ba a gidan su rahman tsautsayi ya fito da ita tun kilama akan layin ne motar ta kade ta har karfe dayan dare bata farfado ba, ya umar yayi tsaki sannan yace wannan 'yar iskar yarinyar ba wata mota yawonta.... momy ta katse shi to sarkn zargi kai da ba ma anan kake ba na kasan tana yawon taja tsaki ta nufi ckin gida tana fadn ni banason sharri wlh , anty tace momy kenan ta dai tana son yarinyar nan , yace kin sani ne anty? can fa na ganta gureran badarawa tana tafe tana hada hanya kamar me maye, to karewa nine na buge ta kuma bany zaton taji wani ciwon kirki ba, anty tace kai haba? yace Allah kuwa shgarta ma in kin gani rin ta manyn karuwai, Allah dai ya shirya

anty tace Amin, yaushe kazo? yace tun shekaran jiya ina nan kd . bani n.d.a bani jaji kin san mun kusan gama course dinnan kuma muna sa ran karin girma ne ,tace Allah yasa yace amin suka shiga ciki
WACECE FARIDA JUMARE?
Farida jumare 'yar asalin jihar yola ce kyakkyawa tamkar balarabiya , mahaifin ta malam jumare mutum ne shi mai tsananin son abin duniya , haka matarshi maimuna.'ya'yansa sune jarinsa don baya yarda dan talaka ya auri 'yarsa. ya aurar da yara 3 kafin farida daya tana aure a abuja anty sa'adatu, any lami tana kano tana auran wani shaharren dan kasuwa ne, sai anty amina da take port harcout mijin ta sojan sama ne mai babban matsayi yanxun burin malam jumare yana kan farida wanda duk tafi suaran yaranshi kyau . wannan yasa ya dage kan tayi karatun zamani don yana da harn shugaban kasa ne, itama farida har tafi mahaifinta kudi , tun tana karamarta take sheka ma 'yan makarantar su karya akn cewa mahaifin ta minister ne, amma da aka gane sai wasu 'yan makarantar tasu suka sa mata farida 'yar minister.
a. secondary kuwa ai sai ta soma bin samari don ta samukudin siyan kayan kece raini,irin na 'ya'yan masu dshi, duk kuwa rin kokarin d yyyinta suke yi na ganin sun fito da ita cikin tsara. ta lakanci maza yanda ba'a zato in taga dan iska ko ince mazinaci tasan shi, tun da in har ta gane yana da kudi sai ta san yanda zata hada hulda dshi manyan mutane take harka dasu tana jan kudi. malam jumare yasan komai amma baya magana tunda shima yana shakar kudi, sai yaga hakan ma ya fiye mishi da ace auran tayi kai har da nasani yayi na cewa suma saura da bai aurar dasu ba tunda wannan hanyar an fi samun kudi (Allah ya kyauta). domin kaf unguwar su babu wanda ya kaishi samun kudi babu mai jan rin motarshi duk lokacn da farida ta smi hutu takan tafi abuja ko port a wani zuwan da tayi ne ta fita farautar masu bayan tayi dan yawonta cikin motar anty amina sai ta zame wani super market

ta shiga ta gama sayendn yan kayan bakinta tafito jingina tayi jikin motarta tana neman lambar wayarwata kawarta 'yaryola da tayiaure anan port. din kanta gama wata shegiyar jeep ta tsaya gabanta kadan
kasancewr idonta yana sanye cikin glass ya bata damar tsurawaa motar ido batare da an gane ba,musmman ma da ya kasance tana mai cigaba da dan danna wayarta ba kyanmotar ko kuma bata taba ganin irin motar bane a'a son take tfa mi motar irin nasu ne? numfashin tane ya soya dauke dan tsabar faduwar da gabanta yayi ba wai don ganin mallakinmotar ya kasance soja ba a' ba kuma ganin matsayin shina sojan ne ya tsorata taba sai dangnin kyau dacikar zati tasha hulda da sojoji amma bata taba ganin sojan da kuma yayi mishi matukar kyau irin wannanba cike (not clear) miskilanci tafiya daga ganinshi tasan zaiyi girman kai , tke sonshi ya shige ta har ta motsa, sun shiga cikin super market (not clear) a motarta ta zauna tana tunanin yanda zata ba da kanta gareshi karo na farko da ta soma tunanin bada kanta ga namiji ba dankudi ba.layin rashi ta soma nema cikin sa'a ksance itama. barikin soja take,a rude tace ganinan ki min taimako,hoton yaumar na nan manne a rana harta isa gidan rashida taimakon waya,
a daddafe suka gaisa ta soma fadin taimakon da zaki min rashida yanzu naga wani gaye shima soja ne kyakkyawa mai mukamn sojanta fari dogo yana da cikar haltta, dariya sosai rashida takeyi kafin tace yaya sunan shi? farida tacenan fa daya, yanzunnan fa na ganshi gskya ina sonshi, ba xan boyemiki ba rashida tace ina zuwa , hotunane na sojoji kusan hamsin amma bataga wanda take neman bahakanne yasa tayi mata alkawarin bincika mata. duk 'yan kwanakin farida babu kwancyar hankali kullum tana zarya gidan rashda ko an samu Ibrn sojanta.yau kam cikn sa'a tana sanye da doguwar riga baka dagyalentakyawunt nakara fitowa tamkar sun hada iri da larabawa , maza da yawasun so tayawa tun kanhanya taki sauraren su,burin ta

taga sojanta , suna ckin hira da rashida a uwar
dakinta wato bedroom , sunusi mjinta y shigo
yana gayamata suna tare da abokin shi ne soja
umar tasan shi sai dai shi ba'a wannn barikn
yake ba tre suka fito tana cewa bari ta tafi amma
me? tana fitowa sukayi ido hudu da sojanta cike
da daga waya dauke kanshi , ta zaun tana gaishe
su msawa daya sojan umar yayi bai kara magana
ba,
amma daya dan gota sai ya gane ta, duk da
kallon tsoron da yayi mata ranar farko, kyawunta
baya da saurin gogewa a idon mutum ya mata
wani duba mai kama dana ranin wayo, kaman
naso na gane ki ko? ta dube shi cikin nuna
kamala da kunya irinta matan kwarai tace
nikuwa? hakan ya birge shi yce gidan sojan
sunusitadan dube shi sannan ta sunkuyar da kai,
hakane. yanzun ma can zanje sai kuma mai
mashine ya kawoni nan barkn yace ayya baki
kulabane? tace eh ban lura ba da yake ma ba wai
ina hawa mashn bane shiyasa duk na kasa skewa
dadi ya kara kamashi dama shi bayason mace
tana hawa mashin yace shigo inkai ki tace a'a ai
nayi dare gida zan koma na jima ina yawo saeda
baya ne na gane bama a barikin nake ba, yace to
shigo nakai ki gidan tace ayi haka kai ma ai kana
da wurin zuwa yayi murmushin da zuciyartaa
kara tsinkewa da kara mustuwa cikin kogin
sonshi yace ba komai cikin farinciki ta shiga.
[1:34PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----7
Gidan anty amina suka je ya ce nanne gidanku?
tace mishi nan gidan yayarta ne, ita yar yola ce
yayi mata yan tambayoyi tasanar dashi duk game
da krtn tane, tace yanzu tana universty,100 lvl
tana karantar home economics, ya ce yayi kyau
hakan domin ina da kishi da yawa ba xan bar
mata ta tayi aiki ba. dadi ya kama ta kenan yana
sonta, dan haka sai tace ai nima nafi san na
xauna a gida dan na kula da mijina da tarbiyan
yayana, yace ba xan bari sai wani lkc ba yaya
sunan ki tace farida jumare,yace farida ina sanki
domin na sami irin matar da na jima ina roqon
Allah ,kanta a qasa wai ita tana jin kunya,

wannan ce farkon fara soyyansu.ya umar yana tsananin san farida yaje yola har ba adadi, kuma yana kashe masu kudi duk da farida tana nuna badan kudin shi take son shiba. saidai wannan bai hana farida hulda da wasu maxan kamar yanda ta saba ba. cikin shekaru ciki ne ya umar yai ta samun matsayi daya bayan daya,har xuwa yanxu dayake saran xai samu muqamin captain. Zahiri farida tana son ya umar, saidai babanta ne bayaso tayi aure sbd kudin da uake narko mishi,amma shi ba dan wani krtn taba.farida ce kawai take ce masa haka.ni ko ayanxu nayi na daman irin shigar da nake yi da, saidai na bar shiri tun rani damin kaf unguwanmu har gidanmu bani da shaida,na daina saka duk wani wando inba na mkrnt ba,ina saka siket ne da xani tun faruwan wannan abin sai naji ina jin kunyan fita.satina daya ko waje ban leqa ba kullun ina kwance.ashe hankalin suraj ya tashi rashin haduwarmu gashi wayar daya bani tana cikin jakar nan,kuma kayan suna gidan su.gashi sanda muka rabu ina pushi sbd abin da yayimin.shi harga Allah ba nufinshi in mun aikata wannan xunubi ya barni ba. a ganinshi wannan baxai shafa auranmu ba.mu qoqarinmu muna koyi ne da nasara wannan shi xaisa mu kara kullewa. kullun sai yaxo layinmu can farkon layin ya tsaya da mota yana sauraran ta in da xan fito.yau ko dayaga an cika sati yar guntuwan wasiqa ya rbt tare da kayan daya saya min.
Har da hotunan da muka yi a gun party da takarmi da jakar, nufinshi muci gaba da mu'amala ta waya, kotsam sai ya hango aisha yar autar mama,can tsallaken titi cikin wani shago,bread taje saya an xubo mata su cikin laida, taxo xata wuce ya tako da sauri ,aisha taja ta tsaya ta dube shi fuska babu walwala tace naam yace ina xaki ne? tace gida xanje, yace asmau tana nan? tace eh, yace taji sauqi ne? aisha cikin qosawa tace eh taji mana,yace gashi in baki saqo ki bata? tace to.mota yaje ya dauko wata laida ya bata sannan kice mata akwai saqo cikin jakar nan xan kirata, har ya tafi sai ya juya

aisha, ta tsaya da sassarfa ya isa gunta kada ki
bari kowa ya gani fa in tana cikin mutanene ki
boye.tace to, bai san aisha da tsurku ba.kai tsaye
dakin mama ta je, tace mama kinga wannan suraj
dinko shi ne ya bani wannan wai in kaima asmau
kar na bari kowa ya gani, mama ta ansa sannan
tace aisha ta
fita.
kwarai hankaln mama ya tashi da taga abubuwan
dake cikin ledar , irin kayan da ta gani tare da
Tunda dai ni ba matarka bace, kuma umar inka damu kasan shi to,ina mai farin cikin shaida maka shine xan aura. alhj sambo ya tsura mata ido.a ranshi yana raya aiko Allah bai qaddaro aure tsakaninsu ba, ta auri wani, baxai so su rabu ba, allah ya kaimu tace amin cikin isa.kuma daidai lkcn wayarta ta soma tsuwa alamar saqon waya ne ya shigo, ta ciro sai taga kiqan sojanta har guda ashirin da takwas tun jiya xuwa yau, koda ta duba sakon sai taga ban hakuri yake tare da lallashi yasan fushi ne ya hanata daga wayar amma ta saurari isowarshi yola nan da qarfe daya. ta dubi lkc qarfe goma ta soma tattara yanata yanata ya dube ta menene? tace babu komai gida xanje, yace bari inyi waya akaiki dan bai dace a matsayina na dan takara a ganni da mace ba, xai iya kawo min matsala ta gefen

abokan gaba, tace bama sai ka kira kowa ba bari
in tafi,ta gama shirya komai sannan taxo
gabanshi yasan nufhnta dan haka ya soma
neman inda ya ajiye check dinshi ya miqa mata,
farida na yaba jiyan.
[1:46PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----14
Dan haka gashi rbt duk yanda yayi miki ta
tsugunna ta rbt dubu dari biyar yace sun isa, tace
i, yace to nidai bana san abin da xai sa mu
rabune, ko kinyi aure, tace dan wannan ai babu
ji.Ina daki sanda ya umar ya dawo daga kai su
anty amarya. nasan hakan ne ta hanyar jin
danayo yana cewa yaran mai suna emeka yaje
but din motarshi ya kwaso plantain, sannan yana
son ganin shi tare da duk masu mishi aiki ma'ana
sauran yan aikin su biyu,mai ba fulawa ruwa da
kuma mai wankin motoci da shara ban da sojojin
masu gadin shi.ban kuma jin duriyarsa ba har
nayi sallar isha na kulle qofata na kwanta. sai fa
da safe nayo wanka na gama shafa mai raina a
cushe ga wata shegiyar yunwa da nakeji ta tun
jiya raina bai gama baci ba, sai da na bude kayan
sawana kaf babu nawa na gida, duka na lefe ne
na dai dauki wani material mai taushi fari mai
bulun fulawa na saka ina daura dan kwali naji
wata irin dukan qofa tamkar xa'a karyata,tsoro
ne ya kama ni na soma tunanin ko wani ne ya
shigo ya umar baya nan?
Amma sai naji muryanshi ce take fadin ke! ke!
malama xo nan ki bude ma mutane qofa, kamar
dakinta,da sauri naje na bude qofar yana tsaye da
wando 3kwata,na kakin soja sai singilet itama ta
kakin ce saidai mai santsi ce, fuskarshi murtuk
tamkar hadarin magariba, ya daka min tsawa
kallan me kike min? nayi maxa na kauda
kaina.yace ta mara kunya yau Allah ya shigo da
ke hannuna, xaki gane kuskuran da nace kada
kiyi, gashi kin qiji kinbi san xuciyarki ta xaki sha
wahala.duk masu aikin nan xan sallame su sbd
abu 2,na farko kema ai yar aikince, sannan inma
na barsu tunda kin riga kinsan dadin maxa to
xaki kafa min xina a gida, dan haka na sallame
su sai ki fito in nuna miki aikin ki,in kinyi kuskure

daya ki sha duka. haka xaki yi ta bauta har my farida taxo kin dinga mata aiki, oya see your eyes Ik a mujiya kina kallona a gurin,qaryan masifa kikeyi, na fito yayi gaba na bishi daga kitchen ya fara, gashi nan xaki dunga maku abinci keda masu gadi kada kisa dani dan baxan ci jagwalgwalonki ba.
Sannan bana san qaxanta kada a barmin kitchen da datti falo a share agoge komai wanke toilet da gyara duk dakunan gidannan.sharangefanmu xuwa mota,sannan kakina dakika jiqa duk dadai basu bane yanxu suna cikin aikinki kina jina ko? hawaye yana xubo min nace to,yace in kin yarda na kamaki da wani kuskure sunanki sorry, ya juya ya fita. a raina nace azzalumi ya xanyi dole inyi tunda iyayana sune suka bada ni dole na haqura. da abinci na fara duk da cewan ban soma sakar mana girki ba ina ganin yanda su anty aina suke yi, dan haka na dafa ruwan tea na soya uban dankali sbd nasaba ganin na gidanmu da yawa,da makunsan ance duk abin da iyaye suke yi ko kuma nace ya mace duk abinda ake yi agidansu krt ne itama shi xata yi a gidan auranta.na gama na soma da dakina sannan falo na shiga kitchen ina gogewa ya umar ya shigo fuska tamke yace ina abincin masu gadin? na bude kula shaqe da dankali da qwai ya xuba min ido cikhm takaici baki da hankali dama nakula da haka,wannan uban abincin fa?
Na xuba mashi ido cikin tsoro yace bar kallona da idanun mujiyanki a gun, na sunkuyar da kai yace ke da wanene wannan dankalin? na ce ta to to ban san yawan masu gadin bane, yaja tsaki ba xan dauki almubaxxaranci ba, dan haka sai ku cinye rar dare ga gun da xaki danna nan xasu xo su amsa ya fita na bishi da kallo yau ne na soma ganin shi da shadda ba kaki ba yar garke ja sai maiqo takeyi. araina nace ga mutun har mutun amma a cikin xuciyarshi mugu ne a mugunta bashi da abokin tarayya. na ci gaba da aikina na gama na fita na share cikin gidan sannan na hau wankin motocin guda uku ne duk na wanke, ban taba wanke mota ba sai yau a gajiye na koma

kitchen na danna gun daya nuna min, sannan na xuba musu cikin wata kular na xuba musu komai cikin jug wato tea dana hada, na basu kofuna ya leqo ta windo ya ce gud mrng madam, na danyi fara'a kadan na ce, mrng naci gaba da aikina ya miqo hannu na bashi ya tafi.na xauna falo na soma karyawa kenan, na dubi agogo sha biyu a raina nace lailai na sha aiki.
A raina nace lalle na sha aiki inko haka xanyi kullun aiki ya same ni, ni asma'u, ina cin abincin nan ina hawayen tausayama kaina,ina gamawa naje na kwanta, wani wawan bacci ne yayi awon gaba dani sbd gajiya ban farka ba sai karfe 2 da rabi ina ganin lkc na duro daga gado na shige toilet wanka nayo tare da alwala na idar da sallah na saka doguwan bakar riga na daura dan kwalin ban ko shafa mai ba sbd bashida amfani in tsaya yin wata kwalliya. na danna kiran maigadi sai gashi da sauri ya ce wldn madam ban ma tanka shiba na miqa mishi dankalin cikin wata kular ya miqo kayan daxun nima na diba na bude fridge, ina neman ruwa, sai naga ashe frixer ne shaqe da kifi,nama, kaji dadai sauransu na komo falo, can soqon tsakanin kujera da kujera naga wani dan mitsilin abu kamar fridge naje amma na kasa budewa.ina xaton ya umar dan kanshi ya aje wannan fridge din tunda daga gefen kujeran xamanshi take, na gane kujeran xamansa ne ta hanyar ganin jaridu da sauran takacan shi a kanta.
Hatta phone landline a gefen kujerar take na koma kitchen na taro a gun wanke wanke na dawo haka na yini iar dare muka cinye wannan dankalin da qwai gyatsar magwas ta dame ni shi dai bansan shigowar shi ba ban kuma damu da in saninba. suna tare da abar sonshi,wanda ta canxa shiga xuwa atamfa yar holan da qaton hijabi maimakon riga da wandon da ta fita dashi, yayi lallashi tare da qara nuna mata tsananin tsanar da yayi ma amaryan tashi tare da qara karanto mata mugayan halayan amaryan,sannan ya labarta mata irin matakin da yayi niyar dauka na axabtar da ita, har sai wuya tasa ta kama

gabanta.farida taji dadin hakan amma bata nuna ba sbd iya bariki, sai tace kar dai a tsananta fa,yace ke dai ki ta mana addu'a baba ya sauko duk randa kika shigo gidan xata bari.farida ta ce iyayanku fa? yace ko ban sake ta ba sai dai ta koma gun su da xama kiyi qoqarin shawo mana kan baba mu samu ya yarda kafin na koma abuja dan Allah ya sani baxan koma abacha barrack da wannan yarinyan ba.ya je yanemi masauki..
Da safe ya zo sunyi sallama in da ya cika su da kudi ya tafi jirgi ya biyo zuwa gida. Tun tuni ya dawo amma bai shigo ba sai 5 ni ko a wannan lkcn na gano wani dan fili can baya gurin da yalwar iskar Ubangiji ba kamar sanyi falon nan ba abu kamar hauka, AC 2 ga fankoki hr 3 bayan ko wani dan couredor na gani kusa da dakina na bi sai naga kofa ina budewa sai naga fili hr da 'yan fulawowyi da kujeru 2 tun da na gama abnci rana dama jalof din taliya nayi,ina gama wanke-wanke na dau abncina na nufi can. A can na yi azahae haka La'asar na kwanta kan sallayar na saka filo sanda ya shigo ya bi ta garejin shi na aje Mota anab ranshi ya soma 6aci sdb yanda yaga motarshi duk jirwaye duka 3n ashe 6acin rai na gaba sai da ya bude motar yaga yanda na lafge motocin da ruwa takaici ya ishe shi ya shigo ta kitchen bai ganni ba ya nufi dakin,shi ne hr toilet bana nan,ya dinga fadin ke ina ki ka shiga ne? Ke sam ni ban ji ba,bam san duniyar da nake ba,ina ta shara baccina ya ce lallai kenan hr ta soma zuwa yawon gulma a mokata don yasan ba za a bar ni fita ba sai da izininshi wato masu gadi hr zai fita sai kuma ya tuna da baya nan take ya zagayo ya fito bayan. Saukar Marin da naji ita ce ta katse min mafarkina da nake yi wai gani ga Rahma a mkrnt muna ta lbr. Firgigit na tashi tare da rike kumatuna tsananin tsoro ne ya ratsani....
Na zaro ido jikana yana rawa ya ce uban wanene ya saka ki ki jika min mota? Cikin in-ina na ce na na na wanke ne,hk ake wankin mota a garinku? Fuu!ya fita sai ga shi ya dawi da belt ya zane ni ya hana ni kuka sannan ya ce in yi ta tsallan kwado,ya fita ya saka direba da maigadi suka kai

motocin gurin wanki ni ko nasha kuka hr na gode Allah da na gaji na fadi a raina ina tuba uwar wuyar da na sha gurin wankin motocin ban ta6a wanke mota ba ban san yanda zanyi ba,shi yasa nayi ta maka ruwa ko ta ina ina sa6o omo,jiya ma haka nayi na zata gida ya kwana yaga sun yi ne shi yasa yau ma na sheka musu ruwa ashe bai ma dawo ba tunda sanda ya fita ban riga na wanke ba. Bai kuma biyowa ta kaina ba hr bayan magriba na rarrafo na shigo ruwan dumi nasa na gasa jikina sannan nayo alwala.A zaune nayi sallah sbd kafufuna sun gaji, nan na kwanta kan abn sallar ina kuka,ni dai ban zo duniya cikin sa'a ba,bn d Suraj da Momy Da Rahma bani da mai sona ina nan hr 8 tayi nayi Isha'i tunda daji ne cikin Inyamurai ban ta6a jin kiran Sallah ba sai dai ka aduba agogo. Asuba ma dan dai jiki ya sa ba da tashi duk gajiya asubahi tana yi zan farka,na idar na koma na kwanta can naji tsawa a kaina,na tashi shegiya ba ki ba masu gadi abincin dare ba? an gaya miki gidana ana yinwa ne ko rowa?

See translation

[1:52PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----15

Nan fa gabana ya fadi na tuna bamma yi girkin dare ba,da sauri na tashi da gani sai zani da hijabin sallah Makaroni na dora nan na zauna a cikin hr tayi na juywe musu na kira su suka dauka na koma daki sanda zan wuce yana zaune kan kujera da dama na zargi cewa tashi ce yana waya da Gimbiyar tashi suna Syy Na gane hakanne ta hanyar kiran sunanta da yayi ya ce Farida my sweet heart kada ki damu na ce ban ta6a ganinshi yana fara'a ba sai yau na wuce daki a raina ina fadin bakin mugu. *************

Haka rayuwata ta kasance cikin wahala da bauta tun ban iya wanke mota ba har na iya, don ya ce ni zan ci gaba da wanke mota in nayi kuskure insha wuya wankin kaki ma na kware hr Azumi yazo ina jin shi ranar wata Asabar da aje saran ganin watan na Ramadan ina goge -goge a falo shi kuma ya na zaune yana shan tea. Da kanshi ya dafa, wayarshi ta soma ringin ya dauka,naji ya

ce Momy ina kwana? Na juyo da sauri tunda na zo nan gidan sai yau naji ya ambaci sunan wanda na sani.tun da ba zama yake ba kamar in amshe wayar in ce Momy ki zo ki cece ni don Allah amma babu hali naji ya ce tana lafiya.
Ai tana bacci bata tashi ba na sanni aka tambaya ya 6ulla min harara na ci gaba da aikina hawaye ya ce duk san da za ki kira Momy bana gida yau kuma bacci take kada ki damu Momy ai zamu zo da sallah in na samu hali amma zaku ga aike na Azumi a raba ma makota naku da na gidan Baba Alhj,kudi zan turo Aliyu ya je ya cire sai a sai komai hr na hidimar Sallah ko? Haka Momy tayi ya nacin son Magana dani amma ya Umar ya ki. Ranar Mndy ko ba ya nan na dauki landline din falo zan kira amma abn haushi ban rike number momy ba, sai fa gidanmu su kam kiran me zan musu suna Murna sun rabu da kaya.Don haka tsabar mugunta ranar Azumin farko dore nayi don ya ki tashina da yake ban san anga wata ba sai da safe na jiyo yana jin Radio ana fada a labarai shine na kama baki duk da ban ci komai ba. Haka Azumin yayi ta tafiya ban san in da yake shan ruwa ba haka sahur. Masu gadi ne kullum sai na musu da rana da safe direba ne kadai ke Azumin shima bn san inda yake Sahur ba,ni dai dama sai dai in na tashi akan lkc in dan hada tea insha in ban tashi ba inyi dore,akwai ranar da har na hada tea saina dubu a gogi naga ashe shida ma tayi ban lura ba kai da Azumin nan nasha wahala mara misaltuwa.
Duk na rame na lalace na fige sai ido a waje na bakin shi yana cewa kamar na mujiya haka hr sallah tazo shi kadai ya tafi kaduna kan ita zuba ido ya ce in shirya shiru sai ma gurin direba naji ya ce Madam Ke ba ki bi oga kaduna ba?Sallah a garin nan ba dadi duk Hausawa sun gudu garin su na ce eh sai ya dawo zan je kai ranar nayi kuka hr na gaji dan nasa rai. Kwananshi 2 ya dawo ina kwance ina jin shi ya turo kofata ya jeho wata leda baka mai dan girma ya juya, na tashi na dubu ledar kayan miyan ne irin kuka, Ku6ewa, da garin yaji da daddawa. Sai Kuma

wata ledar mai dauke da wasu tarkace kamar magani sai wasu wasiku guda 2 daya daga momy daya daga Rahma, na rungume wasikun ina kuka na soma duba ta momy. 'Yata ina fatan kina Ify? Na yi kokarin jin Muryarki amma soja ya ki, Sai ina ganin kamar yana wahalar da ke ne kada ki damu ina nan zuwa cikin watannan zan sa Aliyu ya rako ni in ganki. YA JIKI? Ya ce Kinyi 6ari kwanaki Allah ya ba da mai amfani sannan ga dan tarkacen mata nan duk kisha da madara sai na zo. Momynki. Shiru nayi ina mmkin Ya Umar,wai nayi 6ari? Kai namiji sai a barshi na ji dadi in Momy tazo kafarta kafata, ba zan zauna ba. Bayan na krnt ta momy, na kuma warware ta kawata Rahma domin itama naga abn da ta kunsa. Sis.....Asma'u Nayi Yi kewarki da zaton ki, Musamman a mkrnt Malamai sun kewarki hr gobe na kan yi kuka idan na kalli gurin zamanki a cikin ajin Islamiya,sai dai na ka ji dan dadi in na tuna Ya Umar mutumin kirki ne rike ki amana. Munyi jarabawa yanzu muna SS1 kuma ni da Ya Usman mun shirya don hr iyaye sun shiga ciki.A kwai labari da yawa sai kin zo bikin su anty Aina'u sauran sati 4,nasan kin sani. Aminiyarki, Rahma. Haka wasikar ta zamar min tamkar Kur'ani, kullum sai na karanta ina kuka ina fadin nima ina kewarki Rahma, ina kewar mkrnt.Rayuwa ta haka ta ci gaba da tafiya hr ranar wata Jumma'a na zauna kenan a falo sai ga shi ya shigo tamkar an jeho shi na tashi da sauri zan gudu dan ya min gargadin kan zaman falo,wata rana ya same ni ina zaune ya min duka sannan ya ce duk randa ya same ni sai ya harbe ni tunda bai hada falonshi da sunana ba. Don haka yau ma na ruga daki ina kokarin rufo kofa sai gashi ya banko na tsaya jikna na 6ari shi kanshi yasan ina matukar tsoronshi sai dai ya ce haushen da nake bashi ko zai kashe ni ba zan ce yayi hkr ba sbd tsabar taurin kai,ya ce ke da karfi na dube shi ya ce bari kiji ina ma dai zuwa ya fita can sai gashi da wata 'yar bindiga nan na soma sakin fitsari sbd tsoro nasan zai iya harbina, ya saito ni sosai,sannan ya kauce ni ya harbi bango nan na dauke numfashi

na na fadi tare da salati ga zatona ni ya bindage ashe bango ya harba suma nayi sai da ya debo ruwa ya zuba min na farka ya san na kara tsorata dashi ina da daga kwance ya ce tashi na tashi da sauri ya ce Momy zata zo gobe kinga bindigar nan?na kalleta ta cikin tsoro ya ce yanda kika ga na harbi wannan bangon ya huje haka zan huda cikinki in har kika yi kuskuran gaya mata halin da kike ciki.
Hawaye na zuba na ce bazan gaya mata ba,ya ce ke ki ka sani dai ya fita kai Soja babu imani. Duk da haka nayi murna da zuwan Momy da wuri na gama aikina ya ce yau ban da wankin mota,nayi wanka nasa sabon kaya wani yalon leshi mara nauyi,dama tun da nazo kayana uku ne, daga jallabiya sai atamfa da wani matarial wannan yayi datti in sa wannan,to wace kwalliya zanyi tunda nazo ko bakin gate ban taka ba,ban na ta6a ganin kowa ba daga shi sai masu gadi suma in sun zo daukan abncu,inazaune a bakin gado ina tunanin yanda zanga Momy,oh Allah yau zan ga na gida. Kiran Ya Umar na ji "'Ke!" Na taso da sauri ya dube ni na dan Ikc sannan ya ce to haka yayi saura ki je ki saka sarka da dankunne kiyi shafe-shafen ku na mata,bana son ki yarda Momy ta gano halin da muke ciki za ki koma kwana dakina hr ta tafi na dube shi da sauri ya ce kada ki zata ko na soma sonki ne ba zan ta6a sonki ba,ya ci gaba zan daure in ci jagwalgwalonki hr ta tafi sannan yanzun in kin gama ki zauna nan falo zanje na dauko su,zan kara tuna miki kada kiyi ka sadar sanar da Momy komai dan nasan kanki zata yi fushi dani kamar yanda kema zan ha da ki da naki iyayan duk da ke baki dama d fushin su ba,amma ki sani in ba kya gidana sai dai ki shiga dny ce war Mahaifinki,ko fa da ki ka yarda Momy tayi min Allah in ta tafi zaka gane kuskuren ki,ya tafi dauko su haka nayi jigum a gabn madubi ina kallo kaina ni Asma'u wannan shi ne a dake ka a hana ka kuka,lallai ban da ya ki ina ganin har da sharri ake koya ma Sojoji, Da na yi kwalliyar sai naga nayi kyau,na juya kwayar idunana da Ya

Umar ke kiran su na Mujiya irin idanun nan ne da kwayar su ke da girma kuma sun fito na sha jin mutune na cewa suna son idanuna,haka Suraj na saka sarka da dan kunne na koma falo na zauna ko in ce nadofanu ina kallon tashar Aljazira ina zaton ahi ne yake kallo ya tashi ya tafi dauko su. Sallamar Momy da Aliyu da Ya Umar ce ta dawo dani daga kallon,da gudu na taso ina tsalle na rungume Momy,itama cikin farin ciki ta ce 'yata Asma'u oyoyo 'yata,sai kyma naga ta ciro ni daga jikinta ta tsaya tana dubana, ta kai hannu wuyana ta shafa ramin kirjina ta ce wannan kashin wuyan fa? Na dubi Ya Umar ya 6allo min harara nayi saurin fadin tun da tunda ya Umar ya amshe tunda tayi 6ari ne nima na kakaro 'yar fara'a na ce eh mana ba?tun Ikcn ne kuma bani da Ify ne ai Momy ta dube shi sannan ta dube ni kin zubar da jini ne?Daga ganin jikin nan naki babu jini na ce eh na zubar na kama hannunta zo muje ki zauna,Momy na ce ya Aliyu sannu da hanya ya ce yauwa Asma'u Ya umar ya ja shi suka zauna Momy ma ta zauna naje da sauri na soma loda musu abnci da na sha kala-kala ga.farfesun kaji ga na kan rago ga farar taliya da miyan kwai ga jalof din shinkafa momy fadi take sannu 'yata da aiki duk namu ne? na zuba ma Ya Aliyu komai ga mamakina sai naji ya Umar yana cewa Madam sbd yau kinga su Momy watan kin manta da ni ko? Na yi dan yake na ce to me zan zubo maka? Ya ce sa min Farfesun kannan na zubo Mashi na koma kusa da Momy nima na saka cokali cikin nata....
Muna ci na kalli Ya Umar ya harare ni,Momy ni,Momy ta kalle shi sai abu yake kamar hararar wasa yake min yana yi yana murmushi,Momy ya ce me ki ka gani? Ta ce Hararta naga kana yi, ya ce ai ita ta sani Momy da da ni ta ke cin abncin yau gulma ta tashi wato ta gan ki,ai Momy za ta ta fine .Ni dai sai naji abn wani banbarakawai wai namiji da Suna Hajara. Yanda na lura ya ji dadin naman kannan sai da ya kara,kun san yin girki yau da gobe kan sa mutum hannunshi ya goge, don haka da ba ma yi a gida

muna gani in su Anty Aina suna yi akan ce muje muna yi musu irin jajjage ko yankan albasa ko su Alayyaho,hakan yasa na riga lura tunda ina sha'awar girki shi ya sa yanzun ba ya ba ni wata wahala.Bayan mun gama na ja Momy dakin muna ta hira na tambaye ta Rahma ta ce ga ma sakonta nan na hotuna ta ce kema ki bata naki, da zumudi na amsa ina dubuwa ina fadin Allah Sarki Rahma ina naga hotunan da zan bata? Momy ta ce ba ku ta6a daukar hoto ba ne? nayi saurin tuna gargadin Ya Umar (Da har zan ce yaushe na samu 'yancin yin hoto)Amma sai na wayance na ce mu da ke cikin bariki anya ma muna da gurin hoto,ban dai sani ba.
Momy ta tsuramin Ido ,Anya dai zamannan naku da soja Baya takuraki kuwa? Ni Naga lalacewar tayi yawa Ne Nace bakomai momy Ko mai yanamin daidai gwargwado, abincima sai yadda Naso zanci (A Raina Nace farin abinci bazan Kona namanshi ba; dakanshi yake duba store da firiza duk Wanda babu xai kawo haka drinks)tace shin kodai yana matsamiki ne? Nace a'a momy sai dai Ko Xaki rokarminshi yasani makaranta,Amma fa kadafa kice ninace fa Sabda namishi magana yace a'a yace to Xan mishi (a Raina Nace Allah dai kasa Yaya ya ambience). Munyi magariba da Isha'i tuwon semo na tuka mana da miyar kubewa busasshiya Ga man shanu dayazo dashi damuna cinema yake cewa momy baban farida nema yabashi sanda yaje yola.momy ta tabe baki haryanzu haryanzu kuna tare da farida? Yace to momy aydama ba matsalar tabace babantane kuma yasoma sakkowa, momy tace to kudai kuka sani nidai bazan yarda da batun wani Aure dai yanxuba, sai Naga kamun ludayin yata a gidan nan, ya cire hannu a cikin abinci Kamar ya'ya momy? Ta ce to ganin farko da zanyi Mata banga tasiriba,ta Kara baki ta rame sai idanu a warwaje .yace tonidai gatanan Ki tambayeta me nake Mata? Don ba a satina hudu da auranmu kikaxoba kafin tasamu cikin Nan Kinga Kyan datayi Ga kiba Kamar tafashe. Amma Tana samun cikin Kullum

muna hanyar asibiti, kaina sunkuye anata keramin karya, momy tace kodai batacin abinci ne? Yace tanaci Badai Kamar daba momy tace itama haka tace Toh Allah ya kyauta sukace Ameen.
A kitchen ya sameni Ina harhada wanke wanke yace ke dakina zakizo kuma karki soma zuwanmin da datti batare da yajira amsa taba ya fita. Bayadda zanyi haka nayyo wanka nashafa turare na dakko kayan Bacci nasaka dama bantaba saka rigar Bacci ba mai ya, na taje gashina danma Allah yasa gashina mai kyaune Amma da yadda ba kitso ba saloon din Nan ay da ya lalace na daure da ribbon na daura zani akan kayan nasaka hijjab na zauna kusa da momy tace tashi Kije gurin mijinki nima Bacci zanyi saida safe Haka naja Mata bargo nakara Ac najamata kofa daidai kofarshi Natasha duk tsoro ya cikani kilafa Yau nasha bakaken maganganu ,na tura kofar ahankali tamkar mai tura kwai na leka yace shigo mana cikin tsawa ya fada, nashiga na Maida kofar narufe natsaya Ina raba Ido Ina kallon shahararren dakin mai mutukar tsari komai nadakin sky blue ne, tundaga gadon har shinfidun xuwa kafet da labulaye zaune yake da Riga da wando na Bacci a gaban computer idanunshi sanye da glass, nazauna kasa gefen kofar Ina karema dakin kallo hoton wata kyakkyawa nagani Tana sanye da bakar jallabiya ta rufe kanta da gyalen, Nan kuwa na tsuramata Ido tamkar jinsin larabawa kusa da hotonta Shima nashine yayi kyau cikin kakin sojoji, bansan yaxo kusa daniba sai dai jinsanayi ya shakoni cikin hijab ya ruko wuyana yajani har gaban gadon, yasaka hannu ya ciro hoton wannan matar yace rike na rike da sauri yayi kasa da murya. Matata kenan farida, yaki ka ganta? Gaya min? Da sauri Nace Tana da kyau Nace shigarfa? ta menene? Nace ta mutunci, yace to mutuncin ya mace kenan shigar musulunci ba irinkiba ya Maida hoton ya dauki filo ya wurga min can sakon gadon da bango je can Ki kwanta Sbda gadona bana kazanta bane. Na kwanta da hijabina sbd sanyin AC na shi yayi yawa.Can cikin dare na farka sai na ganshi yana

ta nafilfilu daga gurin da nake ya juyo min baya ne,na tsura mishi ido.Ya Umar yana da kyau ashe yana da Ibada sai dai mugunta,o Allah ban koma baccu ba har sanda naga ya gama ya kwanta,ya dauki waya ina jin shi ya lalubo abar son tashi hira suke ta masoya ina zaton ana nema take gaya mishi zata je fatakot dan yin shawara da Anty Amina game da batun Auran su,shima ya nuna jin dadin shi da yin haka sunyi sallama in da yake ce mata ta yu mafarki mai dadi yana kashe murya tare da kwantar da ita,hr mmkn shi na riga yi, bacci ya sace ni naji an shure ni na tashi firgigit! Tashi kiyi sallah har naje Masallaci na dawo kina nan kina aikin bacci,tun jiya ko juyi ba ki yi ba,kina ma sallar kuwa? na daga kai alamar Eh. Na tafi ina mmkin ashe akwai Masallac ni dai bn ta6a jin kiran sallah ba,naje zan shiga bayin shi ya ce wa?Maza na ki yanda cututtuka suka cika gari? Na ta fi na yi sallah sannan na gaida Momy na shiga kicin.Satin Momy daya suka soma shirin tafiya,kan su tafi sai da ta ce lallai ya Umar ya nemar min mkrnt ya ce zan shiga amma sau mun koma Abuja,sbd nan duk sai a hankalu,mkrntn haka su Momy suka tafi suka bar ni da kewarsu,na koma kamar da uban aiki ga masifa in nai kuskur naci duka da gwale-gwale cikin haka rannan ina fashin sallah na kira masu gadi ta hanyar dannan kararrauwar kar6ar abinci su,daya yazo na bashi naira 500 na ce ya siyo min always,kudin d Momy ta bani dubu biyu,ya dawo kenan sai ga Ya Umar ya tambaye shi menene? ya zo nema ya ce na aike shi ne ya amshi sakon ya shigo dashi ya duba yaga always,ya ce dama su kike aiki siyan wannan abn? Na ce na'am ya ce ina wasa dake ni,ina ina miki mgn kin ji sarai ki dinga wani na'am sai kin sani na ce au ba da shi nake amfani ba tsumma ne nake amfani,ya ce to yanzy ina kika samu kudi ko kin soma sata ne? Da sauri na ce a'a Momy ta ba ni ya ce to bani su na ciro na bashi ya wuce,haka na zauna gidan nan kullum addu'ata Allah ya kawo karshen zamana a gidannan.

Ni ban sani ba ashe tun da Farida taje gurin Antynta Amina ta mata fa da ta ce ki zauna rayuwarki ta kare abn maza su in ba ki sani ba da kin tsufa shekarun ki sunja shi kenab sun gama yayinki gara ki je ki bude wuta ta ce to ya zanyi da shi na gaya mishi halin da kuke ciki zai goya miki baya to ko je gurin Baffan ruga wane ga baban nasu kuma ya bata dama ta turo mai sonta nata don haka ta kira Sojanta kuma ya amsa sun gana da Baffan kuma an ce tura manya yaje ya samu Abba,Abba ya ce ba ruwanshi da wannan mgn,sai ya nufi gurin Alhj, Alhj kam ya goyi baya shi nema ya shirya ya nufi yola inda aka yanke mishi sadaki dubu dari nai ga tsadar ta ba tunda ya san zauki Amarya dal a leda ana mishi tunanin an saka rana wata 4 a lissafe september kenan biki zai kama. Duk da gargadin da momy ta yi ma Ya Umar ya barni in zo bikin su Anty Aina sai ya ce mata to tana tafiya ya ce in dai ban yi kiba ba ba zan je ba.to ban ma san takamaiman lkcn bikin ba shi dai nasan yaje.A kwna a tashi gashi mun shiga October shekara daya da wata kenan da yin auranmu kuma lkcn ne ya Umar ya gama course din shi tun dare ya ce min na shirya kayana washe gari muka dauki hanyar Kaduna a mota.Direba ya jamu ya mu gun ja min kunne kan cewa kar na sake aji wata mgn a bakina,ni dau farin cikina zan je gida..
[1:53PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----16
Duk da ba sona iyayena suke yiba,hakan ba xai hanani shiga na gaishe su ba.mun cika mota da tsaraba sai gurin isha muka iso duk da shegen gudun da mukeyi tare da sammakon da muka yi amma sai da mukayi dare.wannan gari da shegen nisa da gudu na shiga gidan momy ta idar da sallah kenan na fada mata ina ta murna nayi sallolina kenan ina cin abinci yau dai jina nake tamkar na fito daga kurkuku.sai ga rahma ta muka rungume juna sai kuka, momy tayi tayi in shiga gidanmu naqi nace saina huta ai suma basu damu dani ba, da yanxu ko yara ne sun turo, in ina wannan maganan momy dry take min tace quruciya ce, haka sanda taje tana ji ina tambayar

kowa ban tambayi yan gidanmu ba, tace baki tambayi su mama ba, nace bayan qilama basuce a gaishe ni ba? momy tayi dry tace sunce a gaida ke mana,dakin antx amarya na kwana ta ciromin sababin dunkuna wai inji ya umar kada nayi kada nayi amfani da kayana, na gane hikimarshi dan kada ace baya min dinki.washe gari na shiga gidanmu bayan na karya.
Hawaye taf idona bansan ko kunan menene ba, haka suka xagaye ni suna min sannu dana shiga dakin mama ina ganin ta na saki kuka, ita dai kallona take nasan raman da bakin dana qara take kallo, yan gidanmu duk sunyi qorafi kan ramata, nidai bakina qanin qafata inji yan iya magana,ina can har dare na tashi na dawo.momy ke cemin ashe ya umar xai yi aure? duk da ba xaman dadi muke ba saida naji daban,nace ai banma sani ba, shine take ban rabarin sunqi yarda alhj ne mai shige mishi gaba nace Allah sanya alheri kada ki damu momy danni babu matsala,nidai ki mishi xancan krt na tunda ynxu abuja xamu koma ni konan kd ne ma ya barni.momy tace a'a babu batun kd yaxo dai ya min magana daya in baxai saki mkrt bane yamin bayani. ya umar ya sha fada gun momy na cewa bai gayan xancen auranshi ba, duk da yayi qaryar cewa baya ran raina ya baci ne,shi yasa yaqi gaya min haka nan tasa shi ya sai min waya mai kyau bansan yana qera gida a kd ba saida momy take cemin ai yanxu an yanke shawara inya gama gininshi na badarawa.
In ya gama gininshi na badarawa nan xa'a min daki,nace au momy dama xa'a min daki? tace xa'a a miki man cae dinma ai shine yaqi,yace a bari sai kun dawo nan arewa naje gidansu anti aina da gidan salima da fatima. rahma ce ta rakani,randa xamu gaida momynta mun ba ta guri layinsu suraj ance tunda kika yi aure iyayanshi sun rasa gane kanshi, amma sun maida shi krt malesia, nace xaije ya qara lalacewa kenan, agaban suma ya bi mata bare wata qasa? tace lallai kam, nace ai ni inda ya suremin daya nuna yanasan jikina, kinsan fa nan duniya na

tsani namijin da xai nuna yana san jikina. rahma tayi dry tace da kenan yanxu ai dole ki sakarma saja.na dubeta wane wai ya umar um ayi sha'ani dai kawai, tace da fatan ba gudun miji kike yi ba? nace rahma dama ina so mu kebe kiji damuwata,sbd anan duniya kece mutum daya dana ke fadama damuwata, kamar yanda kema nasan duk damuwarki, tace hakane, na kwashe komai tsakanina da ya umar na gaya mata sai da tayi kuka,dan tausaya min sannan tace cabdi yanxu tao ke a wace tuqa kike,
Kada fa kije gashi yanxu shi da matar shine suyi ta cin xarafinki? nace ai ina ganin xan gaya ma abba ne qila ya kashe auran nan tunda sam baya qaunata, bakiga yanda na dawo bane? tace yanxun ma aikin danyi kyan gani,amma batun gaya ma abban shi ba ita bace mafita,sbda yana nuna yana kula da ke sannan yana nuna sanki gaban mutane, ta ki barshi shi da Allah ba azzalumin bane,akwai ranar qin dillanci yanxu dai ki sa krtn ki samu ko can abujan ne,in kin tafi ka kya gidan ma bare kiga haushi,in kin dawo kina daki,nace Allah na tuba rahma haushin me xanji naga nifa ba sanshi nake ba ina ruwana da matarshi? tace to sai abu nagaba.addu'o'ikin shagala da yin nafilfilu,nace acan ina san tashi amma ba xan iya ba naci aiki na gaji kamar jaka, tace yanxu sai ki tashi kiyi ta addu'a,Allah ya kawo miki sauki
Nace hakanne magani na gode. tace,ai ni ma xan dinga taya ki addu'ar, Allah ya sani ina sanki da ya umar saidai kuma yanda Allah yayi ba makawa, na harare ta sannan nace dube ki kema xaki shiga layin masu cewa yana birge su ko kuma yana da kirki ne? tayi dry sannan tace baxa ki gane abin da ake nufi bane.momy ta matsa mishi da maganar mkrnt, hakan yasa shi nema min ta kwana gayamin yake wai shi ba xan je in hana shi sakewa da amaryanshi ba,gara in tafi ta kwana.sannan yace turkish na kaiki, in har baki tsaya kinyi krt ba Allah ba xanyi asaran kudina ba, wuya xaki sha kin sanni,kuma kika yarda kika yi wani abu na bata suna ko kibi maxan da kika

iya dan akwai maxa a mkrnt saina saka bindiga na dauke ragowan nunfashinki duk mu huta,saura kuma idan momy tace kina san mkrnt kice a'a ki gamu dani.shi ke surutunshi amma ni ina maimaitawa ne a raina ina qarawa turkish ni asma'u a turkish? cab! komai yana da hanya,amma da kamban sa rai ba.momy kam tayi fadan yaya xaikai matar aure mkrnt kwana? nace nidai zanje momy inason ta Allah.momy ta yarda cikin kwana kalilan ya gama min komai yace ya aliyu ya kaini momy taki yarda ta matsa mishi saida ya bar komai ya kaaini. da duk abin da dangata yake tafiya dashi makarantar saida komai ya kammala sannan suka tafi don haushina ko sallama bai min ba, ya alyune muka yi sallama dashi na zauna bakin gado ina kallon dakin namu kato ne mai dauke da gado 4 mu 4 kenan . dakin ga kafet labulaye ga ac ga kumafankalafyayyun gadajantamkara gidan uwarkaniko gidanuwatama ban da kamar shi saurn 'yan dakin suna gurin wasanninsu domin yau lahadi duk daliban na. ga suna gurin wasanni. cangurinsha biyu da rabi saigasu sun shigo duk sa'nninane gasu masu kyau, suka bi ni da kallo nima sunake kallo,suka kalli kayana dake lode gefe daya suka kalli juna. dayar ta taso ta zauna gefena tace sannu da zuwa turkish, dyar dake can itama tazo sannu da zuwa wannan dakin namu, itako dayar gabana ta tsugunna tace shin 'yaruwa yaya sunanki? nace ni asma'u ahmad , kufa? ta gabana farar ciki itsce ta soma fadin sunana Amina turaki, mahaifina mataimaki nega shugaban kasar nan, ta gefen dama tace ni ko sunana bilkisu salis marfa, mahaifina shine ne gwamnanjigawa a yanxun ta gefen hagu tace fatima shehu, ni daya ce daga cikin jikokin shehu barno mahaifina shahararren dan kasuwane.
da fatan zaki saki jikinkidamu tare da bamu goyon baya mu zama aminai,nce hakana fiso kun tabajin inda zaman makaranta yafina gida? is gurina kan na hada watana maida jikina nayi kyau red house duk muke dasu mina haka muke. kiranta tuni house captain ta zabeni a

saurauniya, duk da kyawawan makarantar kokarina yasa kawayena like min, har ma da yan class ss1 n shiga lokaci guda sunana ya koma sarauniyar , duk cikin mkaranta muna da abokai maza yan class duk da bana shigemusu amma muna taimakon juna. zama da su mina yasa na goge har na manta da duk wani bacin rai,ban taba tunann akwae ranan da zatazo har inyi dariya ba, dana zata dariyata takare . ashe bahakabane, yau gashi masifataa ta dawo yanga da tsiwa duk sun dawo,dama gasu mina 'yan jan aji sai nace mana group dinmu yan jan aji mun cika girman kai. bana mantaa lokacin inter housee na yarda naci sunan queen.wayyo Allah shigar da yan red housesukayi da shirin da captain dinmu ta min zuwa farentinmu, mun burge mu nemuka zo na daya.ya aliyu da ya usman ne sukazo min su kansu sun yaba da shigar queen. mune mukazo na daya sunce min ya umar ne ya turo su dan an mishi waya ana son iyayenmu suzo muyi a gabansu, shine ya turo su, don shi suna ta shirin biki yana zarya tsakanin yola , kd da abuja
sunyi kayatccen biki irin na masoya , amarya tasha kayan matsi duk dan ta hade kada ango ya gane wani ya riga shi bin hanyar. akwatina 12 dam da kaya masu tsada haka aka diba zuwa yola, a ranar jajibarin daurin aure suka shirya wani shegen lunchin kusan duk wani saurayin ta ko nace abokin shashashancintaya halarta in ka dauke alhaji sambo wanda kishi ya hana shi zuwa, kuma yace to zo suyi na ban kwana kafin nan da ta tare gidan mijinta, inko taki zaiyi yanda mijnta zai gane. haka nan duk ya daga mata hankali gurin lunchin din sai waya yake mata . ango ya damu da tambayar wake ta kiran haka? tace mutane , ta kashe wayar. da dare suna tare da sojan ta har zuwa sanda ya tafi masauki sannan ta kunna waya. alhaji sambo ya kira yace ta rufa ma kanta asiri tazo yanzu inko ba haka ba zai shirya mata tuggu, dole taje gareshi cikin wannan daren ya kwashi garar da akayi wa ango tana ji sai da safe ta dawo gida, bataso haka ba

duk da yawan kudin da ya bata , haka daai ta kara wasu 'yan shirye shirye , an daura auren bayan sallah azahar kasancewar ranar asabar ce, ya umar jin shi yake yau tamkar sallah sunyi dinner katafariyar dinner da abokanshi suka c burn shirya mishi tun bara yace musu auran ya mutu su bari sai zai yi wani su al-amin manyan abokai sai yanxun suka shirya da ya umar sbd yanda yayi mishi tonon silili lokacin. auran mu, yayi ta tura wa yayita turawa abokan su na ko ina da batun auran. son ya umar lokacin ayi komai a boye .amma sai alamin ya yayi ta mishi tallata a waya wannan ya kawo musu dan sabani sai fa yanxun daya wanke kanshi gurin bingimbyafi, yayi duka d aeso boki yayi agun. sai dai farida bata kwanta mishi ba, duk kyanta nashi gurin kyawu in ya cika yawa hadari ne.
*amma sai al-amin ya yayi ta mishi tallata a waya wannan ya kawo musu dan sabani sai fa yanxun daya wanke kanshi gurin bikin gimbiya , yayi duk abin da akeso aboki yayi aagun. saidai farida bata kwanta mishi ba, duk da kyanta nashi gurin kyawu inya cika yawa hadari ne.***
hafis lady ta dubi farida amarya tace in fata kin gama amfani da duk kayan da inno ta hada miki? farida tace ke dai bari,kinsan Allah , saida na gama komai dan iskan nan ahj sambo ya rusa komai, da sauri hafsi lady ta mike tana fadin amma ke farida Allah yayi 'yar iskar baiwa, yanxun dan jaraba da rashin hakuri ke da za'a kawo gidan miji sabon jini shine kikaje kika mika kanki ga wannan tsohon ya shanye duk dan tattalin da tanajin da aka ma ango? farida ta dubi aminayarta ta cikin damuwa tace wlh kawata ba da son raina bane bana ce miki yana ta damuna da waya ba? tace bana ce miki kada ki daga wayar ba? tace in ban daga damun da yakemin dole na daga, cemin yayi in har banzo munyi na bankwana ba , zai min tuggun da soja zai gane kinsan ko ba zan so haka ba. hafsi lady tace me ya hana ki kira ki sanar dani? yanda kike son soja haka yake son mulki sai kice mishi kema zaki fito ki fada ma 'yan jarida alakarku tace kash,

duk tunanin baizo min ba , to yanxu na danyi amfani da wasu, tace inma ya gane ki hada da kissa da kuma kisisina, sai kice fade aka miki tun kina karama, inko bai gane ba ki share shi. farida taja filo tace aiko kin kawo shawara kawata nasan zai gane yanda yake kurin ya auri salihar mace ya sameni fanko dole hankalinshi ya tashi sukayi dariya sannan suka tafa
hafsi lady tace sauaran yanda kike son shin nan ki nuna zakewarki da zalamarki zai iya ganewa, kiyi ta nokewa kina....sllamarango da abokanshi ya katse hirr tasu, nan take farida ta ja gyale ta rufe fuskarta,sun gais bayan barkwanci aka sai baki haka ango ya raka abokanshi sannan ya dawo. sun gabatar da sallar ma'aurata yayi 'yan tamboyoyi game da addini babu (not clear) dama ya zaci haka kasancewar ta kamila a nashi tunanin. soyayyarshi ya shiga nuna mata tare da wasanni tana nokewa tare da nuna tsoro hakan yasa shi binta a hamkali, yana da ilmi musamman na fikihu yasan sirrin mata da yanda halittarsu take hakan ya shiga bin komai a sannu amma sanda ya kai kofar da ya jima yana raya ma ranshi yanda zai bude ta, sai kawai yaji ta a bude, hakan ya saka jikinshi sanyi take komai ya lafa, ruf da ciki ya kwanta sai yana ji tamfar mafarki, kuka ta saka tana fadin innalillahi wa inna ilaihir raji'un dama nasan haka zata kasance a kaina, ya daure ya dube ta amma ya kasa magana, ta mike tare da neman kaya tasaka sannan ta dauki gyalenta ta rufa ta tsugunna gaban gadon inda yake kwance ka yafemin kuma Allah ya baka hakuri nasan ban caacanci ka zana dani ba ta mike zata fita yayi karfin hali ya tashi zauna a kua bakofayc z n,ta jyo fuskashi tamkar bai taba dariya ba gaban ta ya fadi.
[1:56PM, 13/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu1----17
Yace xonan ki gaya min dalilin bada kanki ga wani,ta soma kuka, ban bada kaina ga kowa ba, ta xauna ta daga kai tamkar mai tunani hawaye na xuba kan kumatunta,tun ina yar shekara takwas wani mlmnm bayan mun tashi mkrnt ya amshi jakata sannan ya bani wasu takardu ya ce

in kai mishi su ofis.bayan na dawo yana qofar ajinmu sai yace in shiga cikin ajin in dauki jakata,ina shiga sai ya biyo ni ya rufe qofa....ta rushe da sabon kuka tankar gaske,taci gaba da fadin ya min fyade yayi kaca kaca dani ya gudu sai da aka min dinki a asibiti,ta kifaka kai tana ta kuka mai ban tausayi,uaji makira,ya taso da sauri yaxo xa rungume ta,tausayinta ne ya kika ranshi yana ji aranshi da yaga wannan tsinannan mutum babu abin da xai hana shi saka bindiga ya harbe shi,daga lallashi ya xarce soyewa,ranshi fes.duk da yaji haushin yanda ya sameta amma haka ya daure bai nuna ba tunda ba laifinta bane,soyayya suka shiga xabgawa a satin inda yaga shi qaramin dan wasane a wannan fannin itace take nuna mai salosalo na soyayya.
Abin ya ta bashi mmk hr ya kai ga tambayarta a ina ta koyo wadannan salon,sanar da shi ta yi ai ma'abociyar karance-karancece, dan haka sai ya yi murna da jin haka ta mantar da shi komai.
dani da ke mkrnt muka gama jarabawa a ka bamu hutu. kamar nasan ba zai zo dauka ta ba na ce Balkisu in direban ku yazo daukarki zai sa min hannu ku sauke ni kaduna.Ta ce in an zo daukarki fa? Na ce bros dina na Abujan nan ne zai zo daukata,kuma gidan shi zai kai ni ni ko ina son ganin Momy,Mina ta ce kai Queen ki tsaya a Abuja nan basa sai muna ziyartar juna ba? Na ce kin sani ne? ba ma shi da shi ne sosai zai matsa min gara in je gurin Momy haka ko direba su ya zo suka sauke ni har gida Murna gurin Momy kamar me musamman ganin yanda na koma.Sun gaisa da Balkisu sannan suka dauki hanyar jigawa ko na ce Kano,Momy ta ce me ya hana Soja yaje ya dauko ki? Na ta6e baki sannan na ce kila ya manta,ta ce wane irin ya manta? Na ce ina wayata ne? Ta ciri min ta ce gata sai kin saka a caji na ce zan kira Rahma ne ta san na dawo.
Momy ta ce ina ruwan Rahma in taje gaida Mama ta kan shigo mu gaisa ai Usman ya yi sa'ar mata,na ce sosai ma ita ce dai ba ta yi sa'ar miji ba,Momy tana dry ta ce shima ai ba ruwanshi na

ce ni kam gare ni ba shi da kirki,Anty ta shigo ta ce 'yan mkrnt hr kin iso? Na ce eh ina yini Anty? Muka gaisa ta ce ke da maigidan ne? Na ce a'a kawata ce suka rage min hanya,Momy ta ce shi ne zai zo ya dauko ta yana fama da Amarya? Ai zai zo ya same ni, Anty ta ce a"a Momy kin san ko bayan ta taho yaje? Ta ce ba wani zuwa da zai yi wannan kawar tata da suka kawo ta tun da daga jigawa aka je dauko ta amma na cikin Abuja bai je ba ki ce yana da niyya.Tunda nazo kaduna bai ta6a zuwa ba,Momy kuma bata neme shi ba don koda ya yi mata waya bata ta6a mishi zancena ba, Ko ta ce yaya ba muyi hutu ba? Ko kuma nazo bai zo ba sannan ta lura bai ta6a kirana ba, don haka ta ce ta san maganinshi. Abbada ya nemi ba'asin zamana a kaduna,Momy ta ce nazo ganin gida ne.Hutun mu na sati 4 ne saboda SS2 zamu shiga rannan na shiga gidanmu mun gaisa da su Mama,sai ga Rahma.
Na ce yauwa kawata,dama ina ta jiranki ne kizo ki raka ni saloon,ta ce muje nima ki biya min na wanke nawa na ce lallai Momy zata ba ni sai dai kije gurin Ya Usman ko ke ma Mama ta baki? Mama ta ce zo gashi Rahma,Rahma ta fita tana dry tare da fadin wasa nake Mama,gidan su Momy shiga na yi wanka ina kwalliya muna hira da Rahma muka ji sallama gabana ne yayi wani mugun faduwa ban san mai sallamar ba,na gama na saka riga da siket na atamfa 'yar Holan mun fito falo Momy ta ce ga kudin gyaran kan na ce dari biyu ma za ki ban. Ta ce rike dari biyar din na amsa zamu fito kenan akayi sallama kofar Momy gabana ya sake faduwa ta daga labule ta shigo,Nan take na gane ta. Faridar Ya umar don bayan hotonta da na gani hr da kalandar su na gani dakin Mama hr da agogon su sanye take da wani shegen leshi wanda kyawunshi ya nuna tsananin tsadar shi. Ruwan madara ne da ratsin ja dan gyalenta shi ma ja, Haka takalmi da jaka na dauke kaina daga dubanta duk da ba son mijinta nake ba sai na ji kishinta yana yin kallon da take min tana tunanin nice matar mijinta tunda duk sauran taga su lkcn bikinta,sannan

taga idon da yake ce mata yarinyae ba kyau ba,sai ido kamar na mujiya....
Ni dai muka fita kofar waje muka yi kici6is da Ya Umar ya dube ni cikin mmk ba komai ya ba shi mamaki ba yanda ya manta dani har ga Allah ya manta da wata matarshi a mkrnt yanzu mai zai ce ma Momy ban ko kuma kallon shi ba na sa kai na fita abina,Rahma ce ta tsaya gaishe shi ta biyo ni me yasa bako gaida shi ba? Na ce yanzu ba da ba ne,ba zan dauki wulakanci ba ko dama don ni sane na jur wani abina. Shi kam da ya shiga gurin Momy sai ya shiga kame-kame yana cewa shi sam mkrntr ba su mishi waya su anyi hutu ba,Aliyu ne. ya dauko ta ba shi ba ne amsar da Momy ta bashi kenan,ta fita daga dakin,Farida ta dube shi Soja na wadda tafi ta yanzu ita ce Asma'u din? ya ce eh kawai shi yasan Momy tana fushi dashi ne don ko gaisawa sama-sama suka yi ta,Ya kai Farida dakin Antynshi sanda na dawo daga saloon na gansu zasu shiga gidanmu.Yanayi tamkar ban gansu da na wuce abina,na samu Momy tana yanka Alayyahu na amshi yankan Anty Amarya tana ciki tana tuka tuwan shinkafa,dama su baka gane mai girki komai tare suke yi.....
Gefen baki suka kwana da farko neman masauki ya ce zai yi a hotel,Momy ta ce duk gidan nan ko can gidan Alhj ba gurin kwana sai ka kaita hotel saboda ta raina mana arziki? To kuje sai da safe a gabn Farida ta fadi haka,nan yake ya gyara musu gefen baki tunda Aliyu baya nan haka nan su Jamila.Jamila da Nafisa suna gidan Anty Salima shi ko ya Aliyu sunyi tafiya da Abba ni dai ina can kuryar dakin Momy koma falo na zauna ba zan ta6a gyara musu gurin kwanciya ba,da safe ma sanda suka shigo na gama karyawa kawaye da Mina Turaki ina jin sanda suka yi sallama yi na yi tamkar ban san suna yi ba,Suka zauna Momy ta fita suka gaisa ya Umar sai hararata yake,na mike na shige cikin daki,ina amsa wayata,dakin Anty suka yada zango karfe 2 suka tafi bai ce ma momy komai game dani ba haka nan nima ban ce kala ba dama bana so ace

in bishi Momy ma ba ta ce komai da hutun mu yana karewa ta mishi waya bai zo ba ba ya turo kudi wai Aliyu ya yi min shopping sannan yajw ya biya kudin makaranta hakan ce ta kasan ce muka koma makaranta......
Tun daga wannan ganin ban kuma ganin ya Umar ba,har muka gama SS2 muka shiga 3 duk hutu Momy zata aiko a dauke ni ta ce ma Abba ita ce na dinga zuwa kaduna saboda in an gama gini shi nan zan zauna, ko da Abba ya tuntua6e shi da wannan batun sai ya ce haka ne don haka ya saka shiriritar gama aikin nima haka na ke so, domin yanzun shi kan shi da zai ganni ba yabon kai ba yasan na fi karfin wulakanci daga shi har matarshi basa gabana na samu labarin an ce tana da ciki amma watan cikin hudu ya zube yanda nake ji gurin su Jamila tamkar zai yi kuka saboda zubewar cikin na ce su karata. Duk da matsatsin fiar da ya Umar ke ma Farida hakan bai hanata hulda da abokan shashancin ta ba,ta kan fake da zuwa gidan Yarta dake nan Abuja cikin ta ma cire shi tayi saboda yana bata matsala da abokan harkarta. Alhj Sambo shi ne ya hada ta da likitan da ya cire mata cikin.
********** cikin Yardar Ubangiji muka kammala karatunmu bayan kammala komai aka bamu kyautuka kowa ya kama gabanshi sai dai abn farin ciki ina daya daga cikin dalibai uku da makaranta ta za6a don daukar nauyinmu,muyi karatun Likita saboda hazakarmu in ka ji ana Asma'u to a kaduna ne Amma Abuja har gobe Queen suke kirana.....
Sai da muka dawo gida na samu Momy zata biki jos danginta na bita muka tafi ansa bikin Hadiza da Shema'u Sai na Ya Usman da Aminiyata Rahma,Hadiza da na Ya Aliyu ne haka Shema'u yaron yayan Mamanta ne Sadik. Tun da biki ya matso ba mu da sukuni kawayena su Mina duk na gayyace sy kuma nasan za su zo. Biki ya yi biki kenan,na musu ankonmu duka don har da su cikin kawayen aana gobe daurin aure suka iso Mina tariga su isowa saboda tafi kusa,sannan Balkisu sanda Fatima shehu ta iso mun gama

shirin tafiya lunchen ko hutawa bata yi ba ta yo wanka muka fito,muna ta shakiyancinmy da muka saba,Kowace direbansu ya kawo ta, don haka muka shiga motar su Mina muka shiga tunda shi direban su ya huta haka muka kayata gurin tamkar taurari gaba kin su Mina baya gajiya da fadin Queen duk in da na bi nan sauran mutune suka dauka Queen-Queen,duka amaran lunchen gurin daya muka hada tunda duk gida ne har angon shema'u tunda ya saba dama dasu ya Usman ni da Jamila mun dauki kwalayan abubuwan da zamu raba ma mutane muna kaiwa gurin ajiye wakafin mu sona rabawa,Anty Saluna ta kira ni nazo ta ce ina aurans Na ce wane aure kuma?Har ga Allah ni ina mantawa wai ni matar aure ce,Har mijin kanshi na manta da batunshi. Ta ce iye lallai Asma'u kin hadu shi yasa ko dan gyale ba ku saka ba,na ce share kin ji har zan tafi Anty Fatima ta ce kishiyarki ta ko zo? Na ce tazo bata zo ba ban sani ba,anty Aina'u ta ce na ganta gab da zamu zo nan na ce ita ta sani ni ina ruwana......
Guri ya yi guri,na rasa duk inda nayi jama'a kallona suke,ga mai wakar ya kama Asma'u Queen ban san da wanda ya sanar dashi sunana ba,Har da fadin Queen din Umar Soja marmari daga nesa,naja tsaki na ce bar hada ni da wani Soka,Jamila ta dauki kafadata ta ce dama tun dazun nake son in ce miki duk wanda ya kira ki zamu dau mataki kanshi,na ce jacan ki bani guri,yanzu nake tashena wannan Sojan ya min Tsufa,don haka duk wanda ya kira ni zuwa zanyi muka saka dariya ni da su,gashi dama muna da wata sara ni da su Mina,in munyi abin dariya mun dara sai muce wa ya dukanmu Jamila ta ce Allah ya shirye ku,Haka aka sha lunchen muka taso muna mota su Mina suka dame ni wai wanene Umar Soja? na ce don Allah ku bar zancan shi nima ban san shi ba,Fatima shehu ta ce ba wani ba ki so nw musan Saurayinki kawai Queen.Jamila zata yi Magana na toshe mata baki amma sai da ta ce musu mijinta ne,na ce kunha nayi kama da matar aure? Muna tsayawa kofar

gidanmu Anty Salima ta miko min yaronta Muslim ta ce don Allah Asma'u ki kai danku gurin Momy,na ce yaron nan kato da shi yana tafiya ga surutu amma sai kuyi ta daukan shi? Ni dai ba zan dau ke ka ba sauka ka taka da kanka.Anty Aina'u ta ce dama ke ai ba ki san yara na ce ku ai yaranky sun cika kuya Anty Fatima ta ce kema in ki haifa kin rike naki na ce ba konai suka shige gidanmu mu kuma muka nufi gidan Abba da kawayena ina rike da muslim sam ban kula ba she su Ya Umar da ya Abubakr ne a gurin tare da wasu daban ban san su ba.Muslim ne naga ya kwance hannunshi ya ce ga Dadyna ya nufi gurin Ya Abubakar.Mina ta ce la ji yaro da wayi yasan Babanshi ko ba Babanshi ba ne?? Na ce Babanshi ne mana Bilkisu ta ce yayanki ne, Na ce shi ne Na farkonmu a dakin mu muka zo gota su yi nayi tamkar ban gansu su ba saboda ya Umar dake gurin sai naji su Mina suna gaishe su, har mun gota naji muryar ya Abubakar yana cewa kE Asma'u zo nan na juya na zo shi nake duba na ki kallo gurin Ya umar, na ce gani ya ce ke har yanzu.....
Kanki bai dana hayaki ba ko? Na 6ata rai ya ce gaba kina kallonmu kin wani dauke kai sama sannan dubi shigarki babu ko dan gyale kin daura gwargwaro a kai gashi a waje tamkar ba matar aure ba ko?Na dubi sasheb ya Umar da gefen ido waya yake amma na kula da kallom da yake min da gefen ido, na wuce ban ce komai ba, Fatima Shehu ta ce wai da gaske kina da aure ne? Na ce don Allah muje ciki. Falon Momy na bar su na shiga dakin Anty Amarya dan na dan watsa ruwa kasancewar gidan bai cika kamar gidanmu ba,tun da nan gidan Maza ne wanka nake na tuno ya Umar da na ganshi yau in har ba zan manta ba yau shekara biyu da wata shida kenan rabona da na sa shi a idona. Ya Allah sam ban ji zuciyata tayi farin ciki da ganin shi ba,duk da cika da kyau da kwarjini da na lura ya kara,sannan ga kudi da ya zauna. Can waje kam ya Umar ya dubi Muslim sannan yasa hannu ya dauke shi tare da fadin zo nan big boy,yayi sha'awar yaron kwarai da

gaske.Yanzu kam ya matsu yaga dan kanshi.
Sakin asma'u baya cikin tsarin shi wayo kurum yake mata saidai yanxun yana ganin dole ne ya sake ta ko dan ta yafe mishi laifukanshi, wata xuciyar tace yaya xaka yi da santa? ya miqe yana xaga dakin ya dubi farida dake ta faman shirga bacci, ya sani yana san farida so na yarda da ganin girma da kuma mutunci amma san asma'u daban ne a hankali ya shige shi kuma har yau yana shigarshi kadan ya rage ya gama xagaye dukkan jikin shi ya xauna bakin gado tare da furxar da xaxxafan huci,sai yace menene maganin xuciyarshi can sai tabi amsa da cewa Allah,da sauri ya miqe tare da dauro alwala nan ya duqufa neman mafita gun Allah.Diamand hospital muka je da momy sunmin awo tare da dubani sunce baby lfy amma jininta ne ya dan hau, wannan kuwa ba wata matsala ce mai xafi ba yawancin masu ciki kan sama haka inka haihu sai ya tafi sun min allura,kuma sunce 3 xa-a min kudin in haihu inna haihu kuma amin 2 dama wai 5ce.ya umar ya saka ma ranshi dani,shine xaisa ya iya haqura dani dan gaka ya yanke shawaran barina kd....
[7:49PM, 17/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu 2----12
Yawancin masu ciki kan samu hk in aka harfu sai yatafi sunmin allura da dabara sun ce uku za ai min kafin inhaifu in na haihu kuma aimin 2 dama 5 ce ya umar ya saka ma ranshi wani sonta dani shine zai sa ya iya hakura dani don hk ya yanke shawarar baring kd inyi goyon ciki bayan na haihu sai ya sawwake min gidansu momy na cigaba da zama kafin cikin ya cika wata 9 kowa tausayamin yakeyi satin yaumar 4 sannan yazo yaci fada gun momy ya ce kiyi hkr tana raina yrny nan bana samun zamane shi yasa hkln shi ya tashi da

ganin yanda na kumbura ciki yayi kato kowa
cewa yake bai taba ganin ciki maigirma irin
wannan ba sukan likitoci sunka hoto sun ce Ify ta
lau hk ma cikina kuma watan cikin 8 bai isa
haihuwa ba ya umar yaza kullum yana hanyar kd
da abj dr ya ce indinga zaga gari hkn yakan
tasani gaba mufita zagaye duk inda muka muce
sai anmin sannu inko ina zaune ne hk zaita
matsamin kafafu su dan saki yanaga min kalamai
masu sanyaya rai inshallahu zaki haihu Ify kada
ki damu kinji? Duk addu'a muke miki cikin
sallolinmu kema kina yi? Me zaki ci? Hk zaita
lallabina wani sa'in har tausayi ya ke bani.
Cikin bacci naji kaman an tsungule na farka da
kyar na sauko daka kangado ba nason nayi motsi
mai karfi momy ta tashi bata samun bacci sosai
bayan gida naji inaji don hk na shiga toilet amma
yaki fitowa dg nan basai ciwo ya matsamin ba na
fito na kafa kai jikin gado momy ta farka da sauri
ta ce yayane asma'u ? Na ce bayana marata zan
mutu momy ta ce kiyi salati da addu'a bari inyi
waya usman yazo ko aliyu atare suka iso aliyu
ya dauke mu nida momy usman kuma yaja su
abba da anty dr na dubani ya ce haihuwa da
saura yanzu ma nasoma nakuda domin ban bude
ba jin hk yasa nasadakar mutuwa zanyi ban taba
jin irin wannan ciwo ba don hk na sama raina
tawa ta kare Shi kam yaumar tun dare jikinshi ya
bashi kd babu Ify sbd mafarkai barkatai da yayi
aranar tun asubahi yake kiran wayata amma
shuru babu wanda ya dauka hankalin shi yatashi
sosai yasan da tana kusa zata dauki wayar ko da
masifa zatai mishi yakasa natsuwa sai kusan
A zaton shi ni ce ya ce Asmy jamila ta ce ba ita
bace ya ce tana ina? Ta ce em tana bayi don
ance kada su gaya mishi ya dan ji sanyi har ya
shirya fita kafin yakai ofis dinsu ya koma kira ta
dauka ta ce bata kusa cikin tsawa ya ce ina taje?
Nan ta dabure tarasa me zata ce can ta ce bari
na nemota takashe wayar ya dubi direba ya ce yi
paking a gefe nan ya nemi momy akashe ya nemi
abba tana ringing ba'a dauka ba ya kira antynshi
akashe duk lkcn su kam wayoyin su suma gida

nan fa hkln shi yatashi zuciyar shi tagaya mishi asma'unshi tarasu nan take ya ce da direba sukama hanyar kd sun iso 11 gidan bakowa sai nafisa ya ce ina momy ? Ta ce na asibitin diamond ya ce shine don iskanci kika cemin asma'u tana bayi? Yana magana ne yana fita don hk bai ji amsa datake bashi ba sanda ya iso asibitin na jigata ba kowa guna sai likitoci yaumar ko gaisuwa baiyi da su momy ba ya ce musu ina nake? Suka nuna mashi dakin haihuwa sai ya shige dr ya ce yanlabe kayi hkr kajiramu waje ya ce madam nima kimin hkr naga matata ya nufo ni ya rungume ni sannu ya ke min tamkar shi nakudar take jira ta tashi gadan gadan amma haihuwa shuru likitoci sun ce dayan rana zan haihu amma har 2 shiru yaumar hkln shi yakai karshan tashi ya ce sumin aiki su cire adan in huta sun ce in ankai 4 ban haihu ba zasuyi min aiki ya fita don yo salla tunda sauran karfina har nakai bana iya koda nishi biyar dai dai anmin shirin aiki yan uwa sai addu'a wasu na kuka kada ma momy taji,
A dakin tiyata wani sabon ciwo ya tashi wani uban nishi nayi sai ga yaro ya fito fit jim kadan sai ga sabon ciwo nan suka gane yan biyu ne suka taimakamin aka fito da ita nan suka fito da yaran don gyara dangi suyi matukar farin ciki da sauka lfy anshiya yara anata murnar ganinsu shi kam ya umar ni yake son gani dr ta ce kada yadamu ana kimtsa nine sun min allura sannan suka kaini dakin hutu bacci nake bansan irin hidimar da nake su ba sanda na farka tara tayi momy ce da ya umar ya taso da sauri sannu asmy kin tashi? Kallon shinake kurum a raina na ce badole kai min sannu ba tunda ka hada ni da aiki sai kuma naji dadi dana tuna yau ko gobe zamu rabu da shi ya ce momy a hada mata tea bari ta wanke bakinta shi yatadani na wanke bakina cikin wani kwanon silba sannan na dan sha tea kadan momy ta ce yarta baki ce ina abinda kika haifa ba? Shuru na mata araina ko fadi nake ina ruwana da abinda na haifa ya umar yaje gadon su yadauko daya ya ce kinga arzikin

da Allah ya bamu asmy na kwanta naki kallon su da momy ta matsamin sai na ce ni ina ruwana dasu
Shuru yayi yana kallona momy ta ce wanna karon zamuyi rigima dake asma'u suka fita fatima na ce yaya babu wani lallash ka bude mata wuta ba'a bada nono ke aka baki? Suka fita yazo gaban gado na ya zauna bakin gadon zcy shi tana har bawa yanzu ma bai san ta inda zai soma ba can ya tashi yaje ya dauko maccan ya zauna kusa dani ya ce asma'u ki hkr nasani duk komai laifina ne kada kiyima yaranki horo da laifin babansu ki bada nonon nan domin Allah ba don ni ba kinga ita macce tanada rauni na dube kasan baka mukayi dakaiba don hk bazan bada nona na ba yanzu ina takarda ta? Yayi ajiyar zcy kinsan zan baki tunda nina ce zan baki amma yanzu kisan zuyi ta jin haushin yan uwanmu zasu tsaneki na soma hawaye wannan karon na shirya na yarda in fuskanci ko wace irin matsala ce kai dai ka sallame ni yamike yana jijjiga yarinya sbd kukan da take yi yasa mata lebanshi abaki ya dan jijjigata sai tasoma bacci ya mannata akirjinshi sannan ya zauna bai san me zai ce mata ba yaje ya kwantar da ita sannan ya fita gurin dr yaje ya bashi bayani kan babies suna jin yunwa mamansu tana fushi ta hanasu nono dry likita yayi sannan ya rubuta kalar madaran da ta dace dasu ya ce koda tana basu nono ba dole ne ya ishe su ba dama sai an hada da madara yaje ya sayo ya kawo nan da nan aka dama masu suka soma sha shi kuma ya koma abj sbd bai sanar ba gashi suna cikin wasu bincike ne washe gari yayi lagos
Nikam har sannan naki bada nono na, kwananmu uku aka sallame ni mukayi gidansu momy dama su abba basu sani ba haka nan momy ta hana a fada ma mama. Ran kwana hudu ya iso da kaya niki niki mota guda tamkar masu kayan tashi, duk na yara ne. Su rahama suka fita da su hadiza kowa baya jin dadi yanda yake ganina rai cunkus, bana cin abinci. Hadiza tace Allah yau sai na gaya wa mama, su anty aina'u. ma da gangan suka yi shiru har alhaji ma sai yaji. Rahma tace

a'a ya umar ne yace likitocin sun ce kada a matsa mata fa! Hadiza tace ba dai ya son ya matsa mata amma na taba ganin mai jego ba cin abinci kuma ba zata ba yara nono ba sai shegen bakin rai? Ni kam dama na kosa su fita tunda naji zuwan ya umar yau kama sai ya sallame ni, ya zauna bayan ya dauko yarinyar. Bansan me yasa yafi daukar yarinyar ba, maman 'yan biyu na same ki lafiya? Banza nayi mishi yace yarinyar nan tana kama dake sosai, shi ya sa nafi sonta. Na harare shi, wannan ba damuwa ta bace ni yanzu damuwata ka sake ni, ban ma kaina adalci ba in har naci gaba da zama da kai. Duk sanda na dube ka ina tuna wuyar da ka bani tare da bakaken maganganun da kasha gayamin amma in ka sake ni zan yafe maka kuma raina ya huce. Ya tsugunnan gabana yanzun to wa zai shayar min da yarana? Wai zai kula min dasu? Nayi murmushi sannan nace ka manta da faridarka? Wacce ta iya yiwa yara tarbiya kuma 'yar masu tarbiya?
Ya zauna kasa, ban da magana a yau amma kiyi hakuri. Nace na daina yarda kana min wayo da yawa, gashi ka samu yaran da kake muradi, san...sallamar mama ce ta katse ni, ina take mara hankalin yarinyar, dan ubanki ba a bada nono ni na baki nawa? Ta shigo bata 'yar ta bata nono ko in tsine mata yanzun nan. Ko kuma ki biyani nawa. Don kin sha wuya su suka dora miki? Ba Allah ne ya doro miki ba? Gani nan tun daga haihuwarki na samu hawan jini amma ban hana ki nono ba sai ke? Kuka na saka su momy suna ta ba mama hakuri tace ba fa zata tafi ba sai na basu nono. Ta dubi ya umar tace kai kuma faruk baka gaggaura mata mari? Yarinya mara jin magana. Ya umar yasa ta cinyata, momy ta ciro nonon ina kuka aka sa mata. Nan ko ta kama sai sha tace, shima yana bacci ya umar don mugunta sai da ya taso shi shima suka saka mishi nono ya hau sha, ranar nayi kuka har da ciwon kai.
Da dare ya umar ya shigo na dan dube shi wallahi duk ya rame. Ya ce me da me kike so game da suna gobe zan koma jibi zamu zo da my

farida saboda tana dubai yau zata dawo, na dube shi ina ruwana da suna? Ni fa babban sunana ka sallame ni. Yace zan sallame ki amma ki bari ayi suna mana! Nace ran suna? Yace da dare ba. Nace shi kenan yace to ki saki ranki ki dinga cin abinci kina basu nono, na ce nifa ba zan iya ba da nonon nan ba. Ya ce ke da su daya ne a raina kinji asmy? Yanda yayi maganar cikin muryar tausayi don haka sai ya bani tausayi.
Ya umar ya kashe kudi da sunan nan tamkar a kasa yake hako su. Ni kallonshi ma nake yi. Akwati saiti daya yayi min guda biyar, zannuwa talatin da shida ga key din mota ta academy 'yar mai kyau sabon sanfur ga hajji da umara sannan ga takardun gidan shi na nan kaduna, yace na wane halak malak ko bayan ranshi ko ba ma tare nawa ne. Alhaji da mama fada suka kama yi wai duk iskancin da nake yi har ya birge shi ya min kyauta haka? Abba da momy cewa suka yi babu ruwanku wannan tsakanin miji da mata ne. Haka yasa ni jin tausayin ya umar nasan yana yi ne don in zauna dashi in daina maganar saki to ni bana son shi haka nan bana son 'ya'yanshi. Farida ma tayi hidina sosai, dangi sunyi hidima da mu. Akayi suna yara suka ci momu da abba, kowa ya wadatu da kayan suna. Rago biyu shanu bibbiyu haka ya umar ya yanka. Daren ranar na jira shi dan ganin takarda bai zo ba har sai da nayi bacci. Ya shigo yaran yaje ya tsuguna gabansu yayi musu adduo'I sannan ya sunbace su, yazo kusa dani ya sunbaci kumatuna sanna ya aje min wata 'yar farar takarda kusa dani, sammako yayi don haka bamu hadu ba, ni kam ban ma ga takardar ba sai da ina karyawa naga takarda na dauka da sauri ina dubawa. Cewa yayi: “ki min afuwa ba zan iya sakin ki ba saboda son da nake miki, ki zabi wani horo mai tsanani wanda kike ganin yafi kowanne horo wahala ki min shi, na yarda in dai zaki janye batun saki. Sannan ki taimaka ki kula mini da yarana domin ki tuna ko ba aure na san zaki iya kula min da yarana don zumunci. Kina da hakuri, ki kara hakurin na gode”.

Tsaki naja sannan na yaga takardar, nace ba zan iya zama da kai ba in ko ka ki wallahi zaka ga wulakanci ganin idonka. Haka mukayi ta yin wankan jegon nan yara kam ko kallonsu bana yi, nono kuma sai momy ta tsaya a kaina sannan zan basu, in ko ba ta nan in dage ince sun sha. Satinmu uku ya umar yazo dubamu sanda shigo suna ta kuka ni ko ina kallon filn dina, kuma ina jinsu dama ko suna kuka sai dai wani ya dauke su ya basu ruwa, har mamakin su momy keyi wai ko da labari basu taba jin labarin shashashar uwa uwa irina ba, kashe TV yayi sannan yayi bedroom, ya dauko su yana duba na ranshi bace. Ban san irin qin da kike min ba asma'u, ko baki sona ai kya so 'ya'yanki. Na dube shi in dai ba zaka sake ni ba toh baka soma ganin takaici ba ya umar. Yayi shiru can yace toh bata nono shi kuma sai in bashi madara, nace bani dashi. Na mika na fita. Innalillahi wa inna ilaihir raji'un kurum yake ambata a zuciyarshi. Haka ya basu ruwa da madara, gashi ba aikin shi bane duk ya bata jikinshi. Sai ga nafisa ta dawo daga makaranta, nan ta taimaka mishi ni kam ina tsakar gida.
Haka muka yi arba'in ko yawon arba'in bamuyi ba su abba suka ce maza in shirya zasu kira mijina a waya mu tarkata mu koma tunda iskancin da nake ma yaran kenan. Inje in ma zan kashe su ne in kashe su. Da na sa ma momy kuka sai tace kada in mata kuka itama tafi son yaran a kaina don haka bazata iya kallon cin fuskar da nake yi ma yaran kuma jikokin da tafi so duk cikin jikokinta, haka na hakura saboda dama gurinta kadai nake ganin fuska yanzu kan yaran nan har rahma tsiya mukeyi da ita. Waya abba yayi ma ya umar kan cewa yazo ya kwashe mu yace toh amma ba cikin wannan satin ba, saboda farida bata da lafiya yanzu ma asibiti zaije kaita. Abba yace assha, me ya same ta? Yace wallahi ciwon ciki haka ta kwana abba yace Allah ya sawake mata. Farida tana ta murkususu tamkar zata mutu, likitoci suna ta bincike kanta, ya umar tare da wasu abokanshi suna ta kai

kawo a kofar da aka rubuta emergency. Kusan awa daya likitocin suka yi ta fita daya bayan daya, duk wanda ya umar ya tunkara sai yace yana zuwa. Daga karshe babban likitan ya fito ya dubi sy ya umar yace wanene mijinta? Cikin fargaba ko ta mutu ne ya umar yace nine. Likitan yace biyo ni office.
Bayan likitan mai suna dacta bashir M ya bashi hannu sun gaisa yace matsalar matarka nake son shaida maka. Ya umar ya gyara zama. Dacto ya bar rubutun da yake yi yasa gindin biron akan habarshi. Kasan matarka tana shan giya? Ya umar ya mike da sauri, dr kace me ne? Kasan me kake fada kuwa? Dr yace calm down my friend. Da yawa matanmu suna irin wadannan dabiun. Ya umar ya katse shi to ni matata bata shan komai sai da coke ina zaton baka san aikinka ba. Ya fita yana masifa ya isko su aminu in da ya bar su. Yace kunji wannan wawan likitan wai farida tana shan giya, kuzo ku taimaka min in canza mata wani asibiti. Likitan yayi kokarin fahimtar da ya umar amma abin ya faskara dan yayi fushi sosai. Aminu da sali kam basu ji wani mamaki ba, domin sun jima suna zargin farida dan dai basu da shaida ne, amma sun taba ganinta da wani alhaji a wani guest house amma sai ta nuna musu wai matar mutumin ce kawarat kuma tare suke da ita ta shiga ciki ne. Su kuma sun san wannan mutumin mane min mata ne. Alhaji jamilu kenan.
[7:51PM, 17/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu 2----13
Special hospital suka kai ta, a can ma sun ce suna zaton tana shan giya. Yace shi fa sam matarshi bata shan ko maltina sai dai coke. Sunce ko ma dai menene take sha to ta daina don ya soma lalata mata huhu da hanta. Sun cigaba da kula da ita bayan yayi waya mamanta tazo daga yola tana kula da ita. Suna nan su momy mota daya sukayi sukaje dubata har tana cewa ina yaranta? A ranar ne momy sukayi maganar dawowarmu ni da yara. Ya umar yace don Allah momy ta samo wata dattijuwa wadda zata dinga

kula mishi da yara saboda ni makaranta. Momy tace ko ba makaranta asma'u bata son yaran nan ya ce tana son su momy kunya take ji. Kallonshi kawai momy tayi sannan tayi murmushi domin yanzu baya
son laifin asmau. Haka akayi momy hajjo ta samo mana daga gombe mace mai son yara da tsafta tun a kaduna ta soma kula dasu, iyakata in ta matsa min in basu nono sau daya a rana. Ina jin nauyin hajjo
musamman da take ce min anty. Banaso amma tace sunan babbar yayarsu gare ni don haka ba zata iya kiran sunana ba. Satin farida biyu aka sallame ta. Yazo ranar sati zai kwana mu wuce sundau, niko in da nake ma bai nema ba ya kwashi yaranshi masu hakuri inji momy tare da nafisa suka fita. Tun dare na
soma shirin kayana kamar yanda momy tace inyi. Ban sallami kowa ba saboda na kula kowa haushina yake ji gidan mu kawai na shiga mukayi sallama. Mama tace dama ina so in gaya miki yarannan
amana ce Allah ya baki kuma ranar gobe kiyama zai tambaye ki yanda kika bi dasu. Don haka kije ke da Allah in kin cuce su.
A mota ya umar yamu da hajjo dasu sayyid da sayyida shine sunan da muke kiran yaran su anty aina'u ne suka samusu sbd sunan momy da abba ne
nima zanshiga baya hajjo ta ce keko anty me zai kawo ki nan ga mijinki gaba? Ya ce a to gaya mata dai hajjo. Na koma gaba nazauna banida walwala har muka kai abj dakina na farko nan naga amaida dakin
hajjo wani daki na kusa dana shi wai shine nawa kenan nida farida mun sakashi tsakiya lallai yana nufin zama zanyi
Da dare ya shigo muna zaune da hajjo tana cin abinci ya ce intagama inje in nuna mata dakinta nima nakosa mu kebe sbd ina son takardata ko ta halin
yaya ne. Na kai ta ta ce don Allah ki lura da yaran sbd dare koda zasu tashi kibasu ruwa na

ce bamai hanani bacci na gwarama ki kauso su nan ta ce to andebo su mun samu yau mar yana gyara musu kwanciya hajjo ta ce dama nazone in tafi tasu ya ce barsu nan hajjo nan zasu na kwana insuyi wayo sai sukoma hannun
ki ta ce to sai da safen ku tafita nashiga na zauna kan kujerar madubi ya dube ni kin watsa ruwa? Na ce ance maka nayi datti ne? Ya ce a'a na ce ba damuwar ka
bane yanzu yaya maganar mu ? Ya ce aike kin cika hanzarine ina son insake ki akwai abubuwan da nake dubawa ne shiyasa kinga yanzu matsalar ki yarannan
sbd su kowa haushin ki ya ke ji hakan bayamin dadi don hk nake son ki daure kishayar dasu na shekara daya sai in sallame ki hkl kwance yanzu amshi wannan ya mika mani wani dogon file wannan ki adana na yaranki ne kowannansu yanada hannun jari tare da
acct din su na bude musu don care dubu dari bibbiyu nace ai kabar su gurinka ko kuma kaba farida tunda dama ita zaka basu ya ce ke nace ki adana na ce bazan amsa ba zanyi magana ya pls na amsa shi
kuma ya fita wai yana zuwa gama shirin bacci na saka rigar bacci na kwanta na ba yara baya ina addu'a ya shigo ina shafawa ya zauna kusa dani shi shirin bacci yayo gajeren wando da rigar bacci mai budadden gaba na dubi kirjinshi gashine kirjin yana sa jin wani yanayi don hk na kauda kaina
ya ce sufa bakiyi musa addu'a ba ban tanka shi ba nayi kwanciyata yayi musu addu'a ya kwanta bayana jikinshi ya jawoni na ce menene
wannan hk? Kasan dai yanzu babu wannan a tsakanin mu ko? Ya ce dama ai shekara 2 na ce yasoma shafata to yau kadai kimin taimako na matsune na ce
ka matsu da me wai baga matarka nan ba? Ya ce ai itama babu lfy na ce gaskiya ni yamanna bakinshi cikin nawa na soma mutsu mutsu amma tuni yasan hanyoyi janye hkln diya macce tuni na manta da
batun ki maka lulu duniyar ma'aurata sai da

komai ya natsu sannan naso jin haushin kaina na
tashi na shiga wanka shima hk yana yana fitowa
ya haukan sallaya yashiga kaim ubanjigi kukan
shi ina bacci cikin dare sayyid ya tashi kuka ya
saka babanshi ya dauko shi kusa dani ya zauna
ahkl ya ciro nono ya mika mashi
cikin bacci naji ana shamina nono na tashi da
sauri yasoma shafamin kai yi hkr kinji kadan zai
sha na ce shine har da sata? Yayi dry basata ba
srry pls
Muna zaune cikin sabon dakin nawa hajjo tana ba
sayyid madara ya umar ya shigo cike da murna
ya ce sannu hajjo suna shan madara sosai ta ce
suna sha
ai yaran nada hkr ya ce sun gado mamansu ne
ya dan dube ni itama uwar tasu akwai hkr na kau
da kai gefe ya ce kuzo ku gaida farida sbd ta
kwanta asibiti
hajjo ta ce to ta dube ni taso muje anty natashi
muka shiga dakinta tana kwance tana waya
ganinmu yasa ta dauko dogon Ibr na ce da hajjo
zomuje ta ce a'a bari tagama hk na hkr sai da
tagama mun gaisheta ta amsa cike da isa ta dubi
sayyida dake hannun hajjo ta ce wakike da
suna ? Zo nan hajjo ta mika mata tare
dafadin ga sayyida nan ni dai nafita na barsu ciki
Kai ya umar akwai shegen wayo, haka yake min
wayo shi ya same ni sannan su sha nono. Da
rana ne ma ba na basu, yace ma hajjo ko basu
sha da rana ba
kada ta damu, suna sha da dare. Ko ran da baya
dakina sai sun sha yake zuwa ya kwanta. In ko
yayi tafiya ne bana basu, komai ma bana musu.
Hajjo ce wankansu, wankinsu, cinsu da shan
ruwansu. Farida
kan dauke su amma da ta samu sauki fa ba
sauran zama sai yawo. Yau ma da take zaune
cikin supermarket dinta kallon matashin yaron
takeyi wanda yake cikin yaran da ke kula da gurin
ta, jin sha'awar yaron ya shiga ranta sosai, don
yau kam za ta neme shine. Sssss ta mishi
alamun kiran 'yan gayu, ya juyo ta kira shi da
hannu. Yazo cikin girmamawa ya dan rusuna tace

ka iya jan mota? Yace na iya madam. Tace to zaka kai ni gidan kawata. Yace toh. Suka fita bayan ta ma mai kula da yaran bayani cikin mota take tambayar shi shi dan ina ne? Yace shi dan taraba ne. Tayi ta nuna mishi hanya
har suka isa maitama gidan su aminiyarta lady. Ta shiga suna ta lido ita da saurayinta, ta kira lady gefe wani yaro ne da na jima ina jin shi a raina, so nake inji
irin nashi kwazon. Lady ta saka dariya yaushe kika tashi ciwo, amma kin koma jarabarki. Toh kin gaya mishi? Tace a'a, lady tace toh ni dai zamu bar muku
gidan. Ta shigo da yaron, ba ta bata lokaci ba gurin nuna mishi nufinta, saurayin mai tashen balaga sai wanda Allah Ya tsare. Take ya yarda da nufinta kuma ta yaba ba laifi, sai dai bai kai mijinta ba. Haka tace a cikin ranta. Allah ka tsare mu da sharrin zuciya.
Cikin haka muka samu 'yan watanni kamar hudu, yara sunyi kwari gwanin sha'awa inji mutane. Suna zama kowa ya gansu sai ya kara dubansu. Tuni na
cigaba da karatuna. Ya umar yace ya kusan soma hutunshi in shirya zai dinga koya min mota. Nayi murna don ina sha'awar tuka mota sai dai ban nuna
mishi ba. Tafiya ta same shi ta gaggawa kuma sati uku zasuyi a can kara benin. Don haka yana ta bar mana amanar yara, nace kai ma kasan ban da lokacin yaranka. Ya bar su ga farida da hajjo sannan ashe ya hada computer shi yana son ta ringa dauko mishi yaranshi kafin ya dawo. Bayan tafiyarshi na lura da wani abu, farida tana son yaran ne na ganin idon babansu. Tunda ya tafi bata kula su. Ni ko bai dame ni ba. Ko hajjo ma ta kula, don haka ta min magana. Nace su suka sani, tace koda yake kema uwarsu kin ki su bare ita da ta gansu a sama taka?
Allah ya shirye ki. Na taba ganin inda ake son uba amma ba a son yara? Na dube ta nifa bana son shi hajjo, tace tafi can 'yar nema, yarinta ko da nake tsohuwar da kike kina son mijinki. Naki

salon son ne
haka. Na dafa kirji. Allah hajjo ba sonshi nake yi ba. Tace ai sai kiyi. Na jima cikin daki ina mamaki, yaya kawai ta min fassara wai ina son shi, yaya ma son
yake? Na taba son suraj amma bana jin zan tuna yadda so yake, me yasa hajjo tace ina son mijina? Naga bana mishi magana, ban mishi dariya amma
tace ina son shi. Gidan aminu muka je yau ni da hajjo, tace zata bini don ta gaji da zaman gidan. Aisha matar salis nan muka same su tare da aminan aminu.
Mun sha yini in da muka sha hira soasai, sai biyar muka bar wuse wato unguwar su amina. Mun dan shiga kasuwa sannan muka yo gida.
A falo na ga dankwalin lace din farida. Na wuce shi, hajjo ma ta shigo dauke da 'yar daya a baya daya a kafada suka yi dakinta. Ina bude kofa na ga sun fito
daga nata dakin ita da wani saurayi, da ganina sai duk suka rude. Ta soma mishi magana kace ma anty aminan zanzo kaji ko? Allah Ya kiyaye hanya. Cikin in ina yace ta za..za su ji. Ya fita da gudu gudu sauri sauri. Ta dube ni tace 'dan yata ne. Na taba baki ba tare da nace uffan ba, na shiga daki ina mamaki. Ba wani da zai zo ta kai shi bedroom in har gaskiya za a
bi ko yaya suke. A raina nace biyu kenan, dama na taba jin hirarsu da kawayenta. Ya umar da ya dawo ya sha mamakin yaran nan. Sayyida har yi take tamkar ya tashi daga zaune ta kamo shi, sai daga
mishi hannu suke yi. Niko na share su. Yau kam ko sannu da zuwa ban mishi ba, nace in shi yasa hajjo take cewa ina sonshi to na daina daga yau. Tsaraba
kam yara sun sha ta, washe gari ya fara hutu. Nan ya shirya mana fita ban ma sani bani da hajjo da yara, tunaninshi daya farida. Amma ga mamakin shi da
yace yana son ya kai yara check up turai sai ta nuna yardarta. Tare da fatan khairan. Nan ko

itama dana tana da fita da alhaji jamilu. Tafiyar da take saka ran
shakar kudi masu kauri, har million ashirin. Alhajin na sonta musamman yanda take yadda yayi luwadi da
ita son ranshi. Auzubillah. Ce min kawai yayi shirya zamu je kd, munyi musu tsaraba na kura kowa yaji dadin ganin yara bul bul, can na samu labarin fita
zamuyi a bakin antyn shi, ban nuna mata ban sani ba.
Zaune nake a falo ina kallo su sayyida suna ta guje gujensu, sam dama ba sa zuwa gurina tunda ko kare gurin mai kula shi yake zuwa. Hajjo tana kicin tana
tuwon masara, tace ta gaji da ciye ciyen nan, nace nima zanci. Ta mana kuka dama muna da su duk momy tana bamu. Farida ta shigo yara suka nufe ta da gudu, suka rike ta. Kinga wani ball da tayi dasu tayi ciki abinta, wani irin kuka mai cin rai suka saki sannan suka shide. Wani abu naji yazo ya tsaya min a raina, ina kallon su tare suka mike a gigice suna
kallona suka nufi dakin hajjo. Na mike da sauri na bi su na kama su na rungume sai naji hawaye yana zubar min, na kwashe su zuwa dakina. Na lallashe su suka kwanta a cinyata sai ajiyar zuciya suke yi.
Baccin wuya ya kwashe su na tsura musu ido cikin jin tausayinsu, nan ko sai naji wani son yarana yana ratsa ni. Jin motsin hajjo sai na zame jikina na kwantar dasu na tashi bakinsu duk ya kumbuta. Ai ko
hajjo ban ba labari ba, don ni zata ma fada. Ranar dakina suka kwana, na rungume su yau ce rana ta farko da suka ji dumin jikin uwarsu. Da safe ni na
musu wanka har hajjo tana min tsiya. Yau kuma ana yi da 'ya'yan nawa ne? Sai da ya umar ya shigo ya same ni ina gyara ma sayyida gashi na raba mata gida biyu, na kama mata da ribbon kalar rigarta da
takalminta. Ranshi kar amma baiyi magana ba

yana Tsoron in yayi magana zan fasa gyaran, yace babyn baba me ya same ku a baki? Nace sunyi karo ne.
Yace iye! Sorry zo nan yarinya na kinyi kyau. Ta tafi tana murna tare da fadin dady sweet ata, na soma shirya sayyid shima kayan shi masu kalar ja da fari tamkar nata. Ya umar yaji dadi, don har kama su nayi suna gulmata shi da hajjo yana gaya ma hajjo don Allah kada ta min tsiyar abinda nayi ma yara kada ma daina dan yasan halina.
Mun dawo da kwana uku muka tafi, england muka fara sauka. Dakin hajjo daban namu daban. Ya umar da mukayi cikin wannan kasa nakan manta wai ba son shi nake ba. Kananan kaya ya kai ni na jibgo abin son raina. Kullum ya sani in tsuke mu tafi shakatawa, a raina na kance ina malumtar? Guraren wasanni mu shiga motocin dake gudu kan kankara, mu hau dokin keke da dai sauran su. Ko ina ina manne dashi satinmu biyu mukayi america sannan mukayi dubai. Watanmu biyu na zubar da karatun da nake ikirarin so na kama bin miji yawo duk da ni ba haka nan na so ba. Muna dawowa na tada ballin saki, haka yayi ta lallabani yana cewa in bari yara su shekara. Cikin yardar Ubangjij watansu goma suka soma tafiya, nan fa nace na yaye su dama ba basu nonon kiriki nake yi ba. Ya umar yace to shi kenan. Na ta da tsiyar saki, yace dai a bari sai ranar lahafi. Dadi naji zan kuma nuna musu cewar ina son ya umar ba haka bane. Lahadi tana yi yace muje kaduna zai zo ya kawo min, sannan ya min godiya har da cewa aikin ma min kokari asmy, ni naja motar sabida a rayuwar mu ta england ya koya min mota, kuma ban sha wahala ba. Sai dai ban taba doguwar tafiya ba sai yau, yau ma don ya riga ya fita ne ni ko naki kiran direba. Cikin yardar Allah muka iso lafiya.
Kwanan mu daya gurin su momy, ya aliyu yasa aka gyara mana gidanmu muka tafi can. Na zauan zaman jiran saki. Wata sabuwa! Ba sai ciwon kirji ya sarface ni ba? Baya, kirji abin babu arziki muka yi asibiti. Wani kayan takaici gwajin

farko wai ina da ciki wata uku. Nace ciki? Wai ciki. Tun a asibiti na mishi waya
nace sai kazo san yanda za ayi dan wallahi dacto yace ciki garan. Kazo sai dai a zubar...ya katse ni, kada ki zubar min da ciki, ki bar ni dai zanzo nace to gara kazo, na sha kuka tamkar wadda ta yi shege. Hajjo fada tayi ta min, washe gari yazo yace to gashi yazo yaya zamuyi? Ina kuka nace zubarwa ce zamuyi. Yace to daina kukan abi mai sauki, shirya muje. Ashe ya kira dr sun hada baki da muka je likitan ya dan dudduba sai cewa yai akwai hadari a cikin aikin wai zan iya mutuwa. Ya umar yace toh fa! Yanzun ya za'ayi kenan likita? Likitan yace mu bari sai nan da wata hudu, zai dai bani magani wanda zai sa abin dake cikin ya rasu, in yaso su sai su sa injin su markade shi. Ya tulo min kwayoyin magani ashe duk na karin jine ne ban sani ba. Naje gida nayi ta sha
har da wuce ka'ida ni dole zan kashe abin dake cikina. Satinmu biyu yazo ya lallabani wai in dawo abuja kada su momy su kula ina da ciki su hana mu cirewa. Kai ya umar sai a bar shi.
Tun daga sannan na kama 'ya'yana, nan na shiga yi musu hidima. Su kuma suka daina zuwa gurin farida koda tana zaune da babansu ne. Dan munafunci sai ta ringa cewa mamanku ta raba ni ku, shi kam sai yace sha'anin yaro ne yaya mamansu zata raba ki dasu? Sai tace toh ba gashi ba tunda ta ja su suka ki ni, nikam wata hudu yana cika na tada balli domin lokaci cikina wata bakwai naki zuwa kaduna don kada ma su ganni da ciki su min tsiya, nan ya shiga lallashina wai zamu canza wani asbiti. Muna cikin haka ranar sai ya shiga dakin shi don ganin shirmen yaranshi da na musu birthday baya nan. Ya tuna da na'urarshi mai dauko mishi komai kunne take. Tun daga can suna kanana ya soma kallon da shirmen kin da uwarsu ta musu ya kan sha dariya yanda take satar kallon yaran a lokutan baya da bata son su. Kwatsam sai dan duhu kan abin kallon can sai ga wani saurayi gabanshi ya fadi yace wanene wannan? Farida ta fito daga dakinta sanye da gajeren wando da kuma bireziya.

Innalillahi yake ta maimaitawa, cinyar yaron ta
zauna shi kuma soma shafa cibiyarta. Ba zai jure
gani ba saboda jininshi da ya hau. Nan take ya
kashe sannan ya zube a gado, sunayen Allah ya
shiga jerowa sannan ya samu sassauci lokacin ne
wayar shi ta soma ruri kamar kada ya daga sai
kuma ya duba aminu ne yace in da hali fito mu
hadu nan area 23 zamu gwada maka wani abu
mai muhimmanci. Kamar kada ya fita, sai kuma
yaje ya dauko mota.
Gidan shakatwar alhaji jamilu suka shiga inda aka
shiga da farida da zuwan kamar minti talatin.
Salisa yana aiki da wani kamfanin ne mallakar
alhj jamilu
shiyasa ya san shi kuma alhj jamilun yana sanyo
salis cikin lamuranshu saboda yanda yake da
amana. Shi yasa ake da ikon shigowa gidan
shakatawar dan wataran anan ake lissafin ko
shawara. Kai tsaye falon suka shiga inda suka
leka dakin barcin inda ya umar yaga faridarshi
haihuwar uwarta ana luwadi da ita. Wa iyazu
billah. Faduwa yayi su salis suka fita dashi.
[7:54PM, 17/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu 2----14
Faduwa yayi su salis suka fita dashi sai da yasha
ruwa laida biyu a ranar amma da yake jarumi ne
sai ya dake. Wata tsana da gami da kyamar
faridar suka shige shi. Tsoron daya ko suna
da HIV tun kafin ya bar asibitin yasa aka mishi
gwaji babu komai tare dashi, don haka yayi ma
Allah godiya. Tara saura ya shiga gida amma
bata dawo ba, falo ya zauna gidan ma babu
wanda yasan ya dawo sai ni ce na fito dakin hajjo
naga mutun zaune tamkar gunki. Na shige tunda
dama ba wai ina shiga sabgarshi bane. Don ko
shi ya sani sai naga dama
nake tanka shi. Tara da kwata ta shigo cikin
hijabinta na sutura, har kasa a ranshi yace
FUSKA BIYU. Ta nufo shi da fara'a. Sorry sojana
kana ta jirana inzo in
baka abinci. Ya daure yayi murmushi kada ki
damu na sani harkar kasuwanci ce to ya
kasuwa? Tace alhamdulillahi mun gode Allah. Ta
nufi daki barina rage hijabin nan. Ya ce to, ta fito

cikin leshi ja hannunta dauke da gwangwanin coke dayan maltina. Kusa dashi ta zauna ta mika mishi maltina, kasha naka in sha nawa. Yace yau nima naki zan sha. Tace
toh bari na dauko maka wani. Yace bani wannan ma ya ishe ni. Ta mike bazan baka ba tana dariya wai ita wasa. Ya gane giya ce ta zuba, yace yau naga abin
ala'ajabi. Ta zauna, a ina? Kuma me ka gani kai da baka cika damuwa da lamuran mutane ba, yace to ai yau nasha mamaki. Wani soja ne cikin wannan barikin
ya kama matarshi da wani, ta zauna da gaske kake fada? Yace sosai ma kuma matar aure kace? Yace Allah matar aure mijinta kuma salihi ne dan tare muke.
Tace innalillahi, kai wannan tayi asara. Ita ko ina zata kai zunubi, kina matar aure sannan kina bin wani? Sojana anya mutane sun san girman zunubin zina
kuwa? Balle matar aure ga hakkin miji ga na Mahalicci? Tir da wannan mata. Kallonta yake cike da mamaki bai san tsawon lokacin da ta dauka tana
cutarshi ba. Yace kinsani my farida yanzun ji nake in ni ne wane mataki ya kamata na dauka a kanta? Kashe ta zanyi ko hukuma zan hada ta dasu? Tace ai
ba zancen hukuma in yana son ya more mata ko ya sake ta dama kaga ai in haka ta faru ba aure. In ya sake ta sai ya barta da Allah ya isar mishi sannu kan hankali sai Allah ya saka mishi da mata ta gari. Ita kuma zata ga karshenta. Ya mike cike da murmushi, shawararmu tazo daya my farida. ya mika mata takardar sakinta uku, yace gashi kinga karshenki, sannan tuni Allah ya min sauyi. Kije Allah ya isa Allah ya isa ban taba zina ba, nagode Allah da bai bani haihuwa dake ba. Yayi daki ya bar ta nan cikin mamakin wannan lamari.
Bansan hidimar da suke yi ba sai dai washegari naga ya shigo da wasu zaratan sojoji sun fita da kayan farida sai kangon dakin. Ga zatona sabon

gida ya gina
mata ta tare tun da naga itace matarsa. Sai dai ganin ko yaushe yana gida na soma zargin ko sun rabu ne? Wata kulawa yake mana wacce tafi ta baya. Kullum
yana lallashina ni kam kara botsare masa nake. Yau dai da muna kwance yace ya min alkawari na karshe da zasuyi ya dawo zai sallame. Cikin satin tafiyan wata biyu zasuyi wata haihuwata zai dawo. Suka tafi dan kwantar da tarzoma tare da runduna karkashinsa. Ranar tafiyar tamkar kada ya rabu da 'ya'yansa. Nima ya rungume ni sannan ya durkusa
gabana wai in yafe masa laifukan da yayi min wanda ya sani da kuma wanda bai sani ba. Cewarshi ko ba zai dawi ba, jikina yayi sanyi nace tunda kace in ka dawo zaka sake ni na yafe maka. Yace kina sona? Na girgiza kai alamar a'a. Ya fita sai wata zuciyar ta ce kilan tafiyar kenan. Sai kuma hankalina ya tashi. Kaduna muka koma kowa ya sha mamakin ganina da
tsohon ciki ga yarana dake bibiyata ko ina na shiga. Yanzu nima gaban kowa nuna musu so nake balle ma da babansu yayi wannan tafiya sai naga tamkar sun zama marayu. Su rahma da jamila suna min tsiya kai matar nan da gulma take, bana son miji bana son miji sai shegen hadama, har kin kunso wani cikin. ban da
ta cewa wai barawo hannun mata, kowa haka yayi ta min tsiyar nan ni damuwata ta dame ni tunanin mijina.
Sai yanzun na yarda da batun su hajjo na cewa ina son mijina domin yanzu na kasa kuzari ko yaushe ina kwance da tsohon cikina ina tunanin mijina tare da
tuno tafarkin rayuwarmu har zuwa yau. Waton yadda na dauki ya umar ba haka yake ba, ba mugu bane wancen karan yaki halina ne da yake zaton ina dashi.
Ko zaman mu na kudu bai taba hanani ci da sha ba. Kuma yana horani ne in nayi masa laifi. Sannan bakaken maganganu da na aikata maganganu ba laifi bane dan ya gaya min su,

tunda ya gane zaton shi ba haka bane fa? Yana kyautatamin, yana tausayamin kuma yana nuna yana sona. Ya umar yana da alheri, sadaka, kyauta, zumunci da kuma adalci. Na tuna sanda ya ba farida jari haka ya siyo min gold na daidai kudin da ya bata yace in ajiye. Na tuno irin soyayyar da yake min a lokutan da muka kadaita don aurатayya. Nayi juyi na rungume pillow na saka dayan hannuna ina shafa cikina wanda muka same shi muna tsaka da soyewa a london. Ina son cikina, na tuno sanda ya umar zai bar gida yaso in fada mishi
kalmar so na kasa, in bai dawo ba ba fa? Nan kuka ya kwace min cikin kukan nake fadin ina son ka ya umar don Allah ka dawo zan gaya maka kaji, ina tsananin
sonka.
Na fito daga wanka na koma ban shafa mai ba na saka kayana ban daura dankwali ba na xari hijabina .tunanina ya sha kaina tun gun wanka nake kuka,yau fiye da wata ya umar babu waya in na kira tashi sai ace min tana rufe, ni kam bai ta ba min irin wannan tfy ba,na fito falo hajja da su sayyada suna kallo catun..
Na xari key din mota,dama motocinshi duka ya xube min keys,ban da tawa, sayyida ta dube ni anty an biki,anty suke kirana dan sunji hajjo tana ce min, na kalle ta xo to muje, na dubi sayyid yaran akwai haquri nace xaka? ya daga kai alamar eh, nace to xo muje, hajjo tace anty ina xaku je? nace gun su momy tace to sai kun dawo, na riqe musu hannu muka fita sayyid yace anty banbino aje, nace a'a sayyid yace dady mun je ko?na kalle shi kana san ganin dady ne babana? ya ce um sayyida tace nima ,sabon hawaye ne ya xubo min ina yin parking a qofar su momy ya aliyu tsaye shi da wani suna magana.sayyid ya ce anty ga uncle suna sauka gunshi suka nufa ni kam ciki nayi da sauri. na tasa momy ina kuka tace me ya faru? hankalinta tashe,cikin kuka nake gaya mata halin da nake ciki tace min dama yacd mata inda xasu je daji nd inyi haquri in Allah ya yarda Ify xai dawo, aliyu

ya shigo da yara nan suka yi ta lallashina har na haqura muka yini sannan muka koa gida.
Yau watanshi 2 cur na xuba ido shiru har dare wasa wasa har sati duk na fita hayyacina ga ciki ina gani tsabar tension ne ya sani naqudan dole, naqudan ma ta jini, tunda EDD dina saura kwana 10, kwana na 3 a asibiti na haihu yaro namiji qato, sai dai na xubar da jini sai da aka min qarin jini, aliyu da usman suka bani, an sallame ni duk da ya bar komai hannun aliyu, cewa nayi baxanyi taron suna ba, abar ni inji da kaina, da kuma damuwata, suna kuwa da su abba suka tambaye ni nace susaka sunan ya umar nasan mun rabu kenan yanda nake yi suma duk na karya musu xuciya hankalinsu suka tashi, kai wasa wasa har muka yi arba'in su aminu ma suna xuwa suna kwantar min da hankali shine mai kawo min Ibrn halin da suke ciki yace har an qara tura su wata rundunar sbd abin yaci tura, sai da qar ya kwantar min da hankali ya kance wai shi suna waya,inma musa sai hajjo tace kada kiyi musu anty kin san fa shima soja ne sai ta yuwu hakanne.
Kwatsam rannan ya aliyu yaxo min da Ibrn sun dawo suna abuja,amma an riqe su sbd xa ayi muru qarin girma.murnan dana ringa yi har mamaki tayi ta ba mutane. sai kuma ahanyan su ta xuwa lagos jirginsu yayi hatsari, mafi yawa sun mutu,ina xaune ina kallan Ibrn CNN da misalin 12,sai ga Ibrn da duminshi,wai jirgi mai dauke da man yan sojojin da xa'ayi ma qarin girma ne ya fadi,jirgin yata so ne daga lagos xuwa abuja,ai ban gama jin xance ba na saka ihu,ashe gida sunji ance kada a gaya min domin hajjo tana musu waya tace gani nan na fadi sume bata san me ya faru ba,nan momy ta saka kuka tace shi kenan wani ya gaya mata,farkawa nayi na ganni a gadon asibiti kuka nake sosai musamman dana ga daukachn yan uwana su momy ne ke lallashina ita da mama,mama tace asma-u ai shi bai rasu ba, nace ya mutu ba kwasan in sani ne,lkcn ma su kansu ba sani sukayi ba,jinina ance ya hau dan haka sukaimin alluran bacci na

samu ya dauke ni xuwa yamma sunji bai mutu ba suna asibitin sojojh dake can abuja.

Su abba sun dugunxuma can ina farkawa na samu Ibr nafa ce saina je aka yi ta lallashina kan in naje hankalina xai tashi ne sbd ko su an hana su gani shi.da qar nayi sati tsabar kukana da rashin cin abinci yasa aka ce su barni inje.da qar suka barni na shiga gun shi.na sha kuka ganin yanda kusan duk jikinshi an nannade shi gidanmu na abuja muka dawo,cikin satin ya soma motsi na liqe a asibitin nike kuka dashi addu'oi jama'a sai yi suke masallata har da isalamiyu sbd ya umar mai jama'a ne ga alheri shi yasa kowa ya damu da ya fara jin sauqi, sai me? duk damuwa da kuma hidiman da nake yi dashi sam baya min walwala ko sakin fuska. da farko na ce ciwo ne amma da yaji sauqi fa? sai dake min tare da shan qamshi, watan shi daya aka sallame shi kuma cikin satin wanda suka yi saura suka samu qarin girma, harda ya umar a cikin wadamda suka samu prmt, kowa nata murna abokai sun shirya dinner mi kam tsoron shige mishi nake, shi kam yana yine sbd kada na mishi xancen saki.

Bayan duk wadannan bidirin yau na fito wanka bayan sallar isha'I yara suna gurin hajjo har da junior. Kwalliya na zauna na soma tsarawa. Yau kam na dauki aniyar nuna ma ya umar ina sonshi. Zan gaya mishi baki da baki kuma zai gani a aikace. Sosai nayi gayu, dakinshi na shiga abin da ban tabayi ba shine zuwa turaka. Sanda na shiga yana sanye da gajeren wando fari sol haka singiletin jikinshi. Yana rubuta wata 'yar takarda. Ina shiga ya hada rai tamkar yaga mutuwarshi, yace yawwa gashi. Jikina ya soma bari nace me zan gani ya umar? Ya dubeni duban wulakanci abin da kika dade kina so ne na baki. Kasa na zube gwiwa biyu ka min rai yaya zaka yi da yarana? Yace ki amsa yaran da dama ba wai kina son su bane ko dama da kika wulakantasu me ya same su? Na rike mishi kafa kada kamin haka. Yanzu ina sonka ina kaunarka. Yace karya ne ke da kanki kin fada. Bakin da yace ki, ko yace so karya ne don haka amshi ni tuni na samu

matar aure. Kingama hoton ta nan, ban kalli hoton ba na amshi takarda na fita ina kuka, na dauki gyalena tare da key din mota yana zaune falo nazo wucewa yace au na manta batun karatu in kina bukata zanfa taimaka. Cikin kuka nace banaso ka cuce ni ka koya min yadda zan soka a karshe ka tsunduma ni cikin kogin sanka sannan ka sake ni, ban yafe ba. Yace haka kika min. Na tafi na rasa inda zan nufa.
[7:59PM, 17/10/2016] 🌹@lh@ji🌹 A R: Fuska Biyu 2----15
Karshe
Gidansu naje a tsakar gida na saka ihu da gudu su momy suka fito dasu anty cikin kuka nake fadin ya umar ne ya sake ni. Saki? Inji momy. Shiru abba yayi, anty tace me ya hadaku? Nace ni ban mishi komai ba shine yace wai ba ya sona yanzun ya samu wata. Momy tace anya bai samu matsalar kwakwalwa ba hadarin nan? Abba yace ku shiga daki bari na neme shi a waya. Muna daki sai kuka nake ba ran ma da nonuwana suka soma zuba wannan alamace ta junior ya tashi, nace momy dan Allah ku bashi hakuri ban san me nayi mishi ba yaace ya sake ni, in ma auren zaiyi ai ban hana shi ba, momy tace to ya isa haka yi shiru, abin da kara firgita ni shine duk wayoyinshi a rufe. Ya kira aliyu ya kai shi gidan ya umar amma maigadi yace musu ya dauki mota ya fita, kwana nayi kuka damke da takarda a hannuna.
143-Da safe kam labari ya kai gidanmu. Abba da alhaji a falo suna tattauna yadda za'ayi. Abba yace anty amarya ta kira ni suji ko saki nawa ne. Ta same ni momy tana ta min fadan kukan da nake ta ce ai yazo ma sai ya kara raina miki wayo. Gara ma ki daure ki nuna bai dame ki ba. A raina nace momy ba zaki gane bane, samun kamar ya umar zai min wuya. Anty tace su abba suna kirana shima ya umar din sunci sa'a ya kunnan wayarshi kuma sunce suna neman shi yanzun nan. Kizo da sakin saki nawa ne? Fuskata duk ta kumbura cikin kuka nace bansani ba. Na dauko takardar kan madubi da zanyi sallah na aje ta don hannuna ta kwana muka tafi har momy tana cewa muje zai ga fushina yau. Muna shiga

yana shigowa, wani kyau naga ya kara min shigar kananan kaya ta kara maida shi matashin yaro ya zauna. Momy dake zaune kusa dani ta zungureni ta baya alamar wai in daina kallonshi. Na sunkuyar da kai can na kara kallonshi sai ya min gwalo. Abba yace yanzu umar abin da kayi yayi daidai kenan? Yace me nayi abba? Momy cikin fada tace ina fa zaka sani, shiyasa nace a caji kwakwalwarshi. Alhaji yace duk ba haka ba, yanzu ta kawo takardar saki nawa ne? Na mika musa. Abba ne ya fara dubawa, tsaki yayi sannan ya ba alhaji. A raina nace shi kenan uku ya min. Na kalle shi ina sabon kuka shi kam dariya yake yi. Alhajin ya mike sun maida mu 'yan iska ne ma yaran nan. Momy tace saki uku ne ko? Alhaji ya bata gashi ki gani itama ta mika ma anty amarya ta fita. Dariya naga anti tana yi ta fita duk sun bar mu. Na dauki takardar a hannun kujera in da anty ta ajemin na soma duba ko saki nawa ne? Sai naga ya rubuta:

144 “Ni Umar faruk na kara nunka igiyoyin aurenmu, ba saki ba yaji. Ina son matata shin tana sona?” Na mike ina kallonshi yana min dariya nima dariyar nakeyi fuskata ga hawaye. Ya iso gurina ya rungume ni na dan mihsi dukan shagwaba a kirji nace kai ko? Yace sorry kin son umar ko? Nace ina sonka sosai. Ta kofar waje muka fita ba tare da na koma cikin gidan ba muka je muka bude sabon shafin soyayya da rayuwa mai dadi.

145 Na fito daga cikin mr biggs ina tare da yarana, sayyida da sayyid 'yan shekara biyar suna dauke da kayan kwalama. Junior yana da saurin girma don ya kamo 'yan uwansa, sai yaron cikin da nake dauke dashi muka nufi gidan rahma. A hanya ya umar ya min waya ina dauka yace kin zama matar general gobe za'a tabbatar damu, sai ku shiryo kuzo akwai shagulgula. Murna ba'a magana. Ya umar yana da sa'a duk cikin wadanda suka samu wannan mukamin ya umar ne mai karancin shekaru. Gurin dinner ne mata suka so su minkwace don haka na manne mishi. Munsha dauka gurin 'yan jaridu da kuma

tambayoyi. Ranar muna kwance wata number sai kiran min miji ake yaba dauka sai naga yana kallona. Ana sake kira na dauka muryar mace naji tana cewa don Allah ka taimaka min ciwon sonka yana damuna, nace sai dai ya kashe ki, miji nawa ne ni daya. Yace haba asmy yaya zaki kashe min kasuwa? Na harare shi na tashi xan fita ya kamo ni Allah ni naki ne ke daya, da ace ina kula mata da nayi goma yanzu. Na dube shi bana son kishiya fa kaji mijina? Zo muyi wata hira mai dadi ki bar batun kishiya ke kina wadatani baki hanani abin da zai sa inji sha'awar wata. Kina wadata ni, zokiji wani story kanwata. Yau asibitoci muka nufa don kai taimako ga marasa lafiya. Ya umar kan ware kudi duk wata uku dan taimaka ma al'ummar annabi. Yace yau zan rakaki asmy nima ina son samun ladan ziyara. Kai fa ke bada kudin gurin 'yan HIV, muka soma a bakin gdon wata mata na tsaya jin tana cewa soja, baiji ba nace ya umar, farida ta fita hayyacinta ta koma kwarangwal. Duk wannan kyan babu shi ya gudu, ta soma kuka tana neman gafara. Yace yau ga sakamakona kuma kinga yadda Allah yayi dake, dama kince da sannau zanga yadda Allah zaiyi dake. Ya fita nima na bishi. Ina dukiyar da ta tara? Ina iyaye da 'yan uwanta? Duk sunki ta da ko itace ma shanawa a dangi. Mu kam soyayya akalar rayuwa, dan iyaye sun miki zabi kada ki ki. So da yawa yana zama alheri.

Tammat bihamdulillah.

THE END!!!